وَمَا لَنَا لَا نُؤۡمِنُ بِٱللَّهِ وَمَا جَآءَنَا مِنَ ٱلۡحَقِّ وَنَطۡمَعُ أَن يُدۡخِلَنَا
رَبُّنَا مَعَ ٱلۡقَوۡمِ ٱلصَّٰلِحِينَ ٨٤ فَأَثَٰبَهُمُ ٱللَّهُ بِمَا قَالُواْ جَنَّٰتٖ
تَجۡرِي مِن تَحۡتِهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُ خَٰلِدِينَ فِيهَاۚ وَذَٰلِكَ جَزَآءُ
ٱلۡمُحۡسِنِينَ ٨٥ وَٱلَّذِينَ كَفَرُواْ وَكَذَّبُواْ بِـَٔايَٰتِنَآ أُوْلَٰٓئِكَ
أَصۡحَٰبُ ٱلۡجَحِيمِ ٨٦ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا تُحَرِّمُواْ
طَيِّبَٰتِ مَآ أَحَلَّ ٱللَّهُ لَكُمۡ وَلَا تَعۡتَدُوٓاْۚ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يُحِبُّ
ٱلۡمُعۡتَدِينَ ٨٧ وَكُلُواْ مِمَّا رَزَقَكُمُ ٱللَّهُ حَلَٰلٗا طَيِّبٗاۚ
وَٱتَّقُواْ ٱللَّهَ ٱلَّذِيٓ أَنتُم بِهِۦ مُؤۡمِنُونَ ٨٨ لَا يُؤَاخِذُكُمُ ٱللَّهُ
بِٱللَّغۡوِ فِيٓ أَيۡمَٰنِكُمۡ وَلَٰكِن يُؤَاخِذُكُم بِمَا عَقَّدتُّمُ ٱلۡأَيۡمَٰنَۖ
فَكَفَّٰرَتُهُۥٓ إِطۡعَامُ عَشَرَةِ مَسَٰكِينَ مِنۡ أَوۡسَطِ مَا تُطۡعِمُونَ
أَهۡلِيكُمۡ أَوۡ كِسۡوَتُهُمۡ أَوۡ تَحۡرِيرُ رَقَبَةٖۖ فَمَن لَّمۡ يَجِدۡ فَصِيَامُ
ثَلَٰثَةِ أَيَّامٖۚ ذَٰلِكَ كَفَّٰرَةُ أَيۡمَٰنِكُمۡ إِذَا حَلَفۡتُمۡۚ وَٱحۡفَظُوٓاْ
أَيۡمَٰنَكُمۡۚ كَذَٰلِكَ يُبَيِّنُ ٱللَّهُ لَكُمۡ ءَايَٰتِهِۦ لَعَلَّكُمۡ تَشۡكُرُونَ ٨٩
يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ إِنَّمَا ٱلۡخَمۡرُ وَٱلۡمَيۡسِرُ وَٱلۡأَنصَابُ وَٱلۡأَزۡلَٰمُ
رِجۡسٞ مِّنۡ عَمَلِ ٱلشَّيۡطَٰنِ فَٱجۡتَنِبُوهُ لَعَلَّكُمۡ تُفۡلِحُونَ ٩٠



**(84) Wane dalili ne sai shiga tsakaninmu da imani da Allah, da abin da ya saukar na gaskiya, wanda Annabi Muhammad (S.A.W) ya zo da shi? Muna fatan shiga Aljannah tare da Annabawa da mabiyansu, masu biyayya ga Allah, masu tsoron azabarsa.**

**(85) Sai Allah ya saka musu da Aljannatai, waxanda qoramu suke gudana a qarqashin gine-ginensu, saboda imaninsu da yardarsu da gaskiya, za su zauna a cikinsu har abada, wannan shi ne sakamakon masu kyautatawa, wajen bin su ga gaskiya, da jayuwarsu gare ta, ba tare da wani dabaibaiyi ko sharaxi ba.**

**(86) Waxanda suka kafirce wa Allah da Manzonsa, suka qaryata ayoyin Allah, waxanda ya saukar ga Manzonsa, waxannan sune waxanda za su lazimci wuta mai ci, ba za su fita ba har abada.**

**(87) Ya waxanda suka yi imani, kada ku haramta daxaxan abubuwa na halal, na abin ci da abin sha, da aure. Kada ku haramta su, don gudun duniya da bautar Allah. Kada ku qetare iyakar abin da Allah ya haramta muku. Haqiqa Allah ba ya son masu qetare iyakokinsa, yana qinsu.**

**(88) Ku ci daga abin da Allah yake koro muku na arziqinsa, na halal mai daxi, ba abin da yake haramun ba, kamar na qwace da abu mai muni. Ku ji tsoron Allah ta hanyar kamanta umarninsa, da nisantar abubuwan da ya hana. Allah shi ne wanda kuka yi imani da shi, kuma imaninku yana wajabta muku ku ji tsoronsa.**

**(89) Ya ku Muminai Allah ba zai muku hisabi a kan abin da yake gudana a harshenku ba, na rantsuwar da ba ku yi nufinta ba. Zai muku hisabi ne a kan abin da kuka yi niyya, zukatanku suka qudurce abin da kuka yi rantsuwar a kansa, sannan kuka warware shi, zai shafe muku laifin abin da kuka yi rantsuwa a kansa, kuka faxe shi da zavin aikata xayan abubuwa guda uku, su ne:ciyar da Miskinai goma, daga tsaka-tsakiyar abincin garinku, kowane miskini a ba shi rabin Sa'i, ko tufatar da shi, da abin da a al'ada ake kiransa tufafi, ko yanta baiwa mumina. Idan mai kaffara bai samu abin da zai warware rantsuwar da shi ba, daga xayan waxannan abubuwa guda uku, to sai ya yi kaffara da azumin kwana uku. Waxannan abubuwan da aka ambata su ne kaffarar rantsuwarku – ku muminai – idan kun rantse da Allah, sannan kuka warware ta. Ku kiyaye rantse-rantsenku, daga yin rantsuwar qarya, da yawan rantsuwa da Allah, da rashin cika rantsuwa, matuqar rashin cikawar ba shi ne alheri ba. Ku aikata alheri, ku yi kaffarar rantsuwarku. Kamar yadda Allah ya bayyana muku kaffarar rantsuwarku haka yake bayyana muku hukunce-hukuncensa, masu bayyana halal da haram, ko kwa godewa Allah a kan sanar da ku abin da baku sani ba.**

**(90) Yaku waxanda suka yi imani, abin maye da yake tafiyar da hankali, da caca wadda kowane vangare za su sa wani abu, da duwatsun da mushirikai suke yanka a wurinsu, don girmama su, ko waxanda suka kafa su don bauta musu, da kibau da suke neman sanin rabon da aka rubuta musu na gaibu da su, dukkan waxannan zunubi ne, daga qawatawar Shaixan ne, ku nisance su, ko kwa rabauta da rayuwa mai girma a duniya, da ni'ima a Aljannah a lahira.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Umarni da neman mai daxi (halal) a arziqi, da barin mummuna (haram). 2 - Ba a kama mutum a kan rantsuwar da babu nufi. Ana kamu ne a kan abin da zuciya ta qudurce, misalin: Wallahi zai aikata kaza, ko Wallahi ba zai aikata ba. 3 - Bayanin kaffarar rantsuwa: ciyar da mutum goma, ko tufatar da su, ko 'yanta baiwa mumina. Idan mai kaffara ba zai iya zuwa da xayan waxannan abubuwan da aka ambata ba, to ya yi kaffarar rantsuwarsa da azumin kwana uku. 4 - Ayar da Allah yake cewa: "giya….." zuwa qarshenta, itace qarshen ayar da ta sauka a kan giya, kuma nassi ce a kan haramcinta.**

إِنَّمَا يُرِيدُ ٱلشَّيۡطَٰنُ أَن يُوقِعَ بَيۡنَكُمُ ٱلۡعَدَٰوَةَ وَٱلۡبَغۡضَآءَ
فِي ٱلۡخَمۡرِ وَٱلۡمَيۡسِرِ وَيَصُدَّكُمۡ عَن ذِكۡرِ ٱللَّهِ وَعَنِ
ٱلصَّلَوٰةِۖ فَهَلۡ أَنتُم مُّنتَهُونَ ٩١ وَأَطِيعُواْ ٱللَّهَ وَأَطِيعُواْ
ٱلرَّسُولَ وَٱحۡذَرُواْۚ فَإِن تَوَلَّيۡتُمۡ فَٱعۡلَمُوٓاْ أَنَّمَا عَلَىٰ رَسُولِنَا
ٱلۡبَلَٰغُ ٱلۡمُبِينُ ٩٢ لَيۡسَ عَلَى ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ
جُنَاحٞ فِيمَا طَعِمُوٓاْ إِذَا مَا ٱتَّقَواْ وَّءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ
ثُمَّ ٱتَّقَواْ وَّءَامَنُواْ ثُمَّ ٱتَّقَواْ وَّأَحۡسَنُواْۚ وَٱللَّهُ يُحِبُّ
ٱلۡمُحۡسِنِينَ ٩٣ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَيَبۡلُوَنَّكُمُ ٱللَّهُ بِشَيۡءٖ
مِّنَ ٱلصَّيۡدِ تَنَالُهُۥٓ أَيۡدِيكُمۡ وَرِمَاحُكُمۡ لِيَعۡلَمَ ٱللَّهُ مَن يَخَافُهُۥ
بِٱلۡغَيۡبِۚ فَمَنِ ٱعۡتَدَىٰ بَعۡدَ ذَٰلِكَ فَلَهُۥ عَذَابٌ أَلِيمٞ ٩٤ يَٰٓأَيُّهَا
ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا تَقۡتُلُواْ ٱلصَّيۡدَ وَأَنتُمۡ حُرُمٞۚ وَمَن قَتَلَهُۥ
مِنكُم مُّتَعَمِّدٗا فَجَزَآءٞ مِّثۡلُ مَا قَتَلَ مِنَ ٱلنَّعَمِ يَحۡكُمُ بِهِۦ ذَوَا
عَدۡلٖ مِّنكُمۡ هَدۡيَۢا بَٰلِغَ ٱلۡكَعۡبَةِ أَوۡ كَفَّٰرَةٞ طَعَامُ مَسَٰكِينَ
أَوۡ عَدۡلُ ذَٰلِكَ صِيَامٗا لِّيَذُوقَ وَبَالَ أَمۡرِهِۦۗ عَفَا ٱللَّهُ عَمَّا
سَلَفَۚ وَمَنۡ عَادَ فَيَنتَقِمُ ٱللَّهُ مِنۡهُۚ وَٱللَّهُ عَزِيزٞ ذُو ٱنتِقَامٍ ٩٥



**91 Shaixan yana nufin qawata muku kayan maye, da caca ne, don ya jefa qiyayya da gaba a tsakanin zukatanku, da kawar da ku daga ambaton Allah. Ya ku Muminai ko za ku bar waxannan munanan ayyukan? Babu shakka barinsu shi ne ya dace da muminai. Don haka sai suka hanu.**

**92 Ku bi Allah. Ku bi Manzo, ta hanyar kamanta abin da shari'a ta yi umarni da shi, da nisantar abin da ta hana, ku kiyayi savawa Allah. Idan kuka bijirewa yin hakan, ku sani isar da abin da Allah ya yi umarni ne kaxai abin da yake kan Manzonmu, kuma ya isar, idan kun shiriya, to don kanku, idan kuwa kuka munana to a kanku.**

**Yayin da haramcin giya ya sauka, sai wasu muminai suka so sanin halin yan uwansu waxanda suka mutu suna musulmai, gabanin a haramta ta, sai wannan ayar mai zuwa ta sauka:**

**93 Babu laifi a kan waxanda suka yi imani da Allah, suka yi ayyuka nagartattu, don neman kusanci ga Allah, cikin abin da suka sha na giya kafin a haramta ta, matuqar dai sun nisanci abubuwan da aka haramta, sun ji tsoron fushin Allah a kansu, sun yi imani da shi, sun tsaya a kan ayyuka nagartattu, sannan suka qara da kiyaye Allah, har suka wayi gari suna bauta masa kamar suna ganinsa, saboda abin da suka ji a ransu na lurar Allah gare su a koyaushe. Wannan shi ne abin da yake jan mumini zuwa ga kyautata aikinsa da gyara shi.**

**94 Ya waxanda suka yi imani, tabbas haqiqa Allah zai jarrabe ku da wani abu na farautar tudu da zai koro shi gare ku, har ya zama kuna iya kama qananan dabbobi da hannayenku, alhali kuna cikin Ihrami, don Allah ya bayyana wanda yake tsoronsa a voye, saboda yana da cikakken imani da ilimin Allah, don haka sai ya kame daga farauta, don tsoron wanda ya halicce shi, wanda babu abin da yake vuya daga aikinsa. Duk wanda ya qetare iyaka, ya yi farauta yana cikin ihramin hajji ko umara, to yana da azaba mai ciwo ranar alqiyama, saboda abin da ya aikata na sava abin da Allah ya hana.**

**95 Ya waxanda suka yi imani, kada ku kashe farautar tudu alhali kuna cikin ihramin hajji ko umara, duk wanda ya kashe farauta daga cikinku da gangan, to ya wajaba a kansa ( ya yanka) kwatankwacin dabbar da ya farauta, daga Raquma ko Shanu, Ko Awaki da Tumaki, wanda mutane biyu adalai daga musulmi za su yi hukunci da hakan, duk abin da suka hukunta za a yi masa kamar yadda ake yi wa hadaya, na aikawa zuwa Makkah, da yanka shi a harami, ko qimar haka na abinci, za a bawa faqiran Harami, kowane faqiri rabin sa'i, ko yin azumi, a maimakon kowane rabin sa'i na abinci, duk an yi hakan ne, don wanda ya kashe farauta ya xanxani uqubar abin da ya yi na kisa. Allah ya yafe abin da ya wuce na kashe farautar Harami, da kisan da mai ihrami ya yi na dabbar tudu kafin haramtawa. Duk wanda ya ci gaba da aikatawa, bayan an haramta, Allah zai kama shi, ya azabtar da shi a kan haka. Allah mai qarfi ne, daga cikin qarfinsa yana azabta wanda ya sava masa in ya ga dama, babu abin da yake hana shi.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Ba a kama mutum da laifin abin da ba a haramta masa ba, ko kuma labarin haramcin bai isar gare shi ba.**

**2 - Haramcin yin farauta ga wanda yake cikin ihramin hajji ko umara, da bayanin kaffarar wanda ya yi farautar.**

**3 - Yana cikin hikimar Allah cikin haramta abu, shi ne don ya jarraba bayinsa, ya tsarkake su. Hikimar kaffara kuwa ita ce tsawatarwa da tsoratarwa.**

أُحِلَّ لَكُمْ صَيْدُ ٱلْبَحْرِ وَطَعَامُهُۥ مَتَٰعًا لَّكُمْ وَلِلسَّيَّارَةِ ۖ
وَحُرِّمَ عَلَيْكُمْ صَيْدُ ٱلْبَرِّ مَا دُمْتُمْ حُرُمًا ۗ وَٱتَّقُوا۟ ٱللَّهَ ٱلَّذِىٓ
إِلَيْهِ تُحْشَرُونَ ﴿٩٦﴾ ۞ جَعَلَ ٱللَّهُ ٱلْكَعْبَةَ ٱلْبَيْتَ ٱلْحَرَامَ (ربع الحزب ١٣)
قِيَٰمًا لِّلنَّاسِ وَٱلشَّهْرَ ٱلْحَرَامَ وَٱلْهَدْىَ وَٱلْقَلَٰٓئِدَ ۚ ذَٰلِكَ لِتَعْلَمُوٓا۟
أَنَّ ٱللَّهَ يَعْلَمُ مَا فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِى ٱلْأَرْضِ وَأَنَّ ٱللَّهَ بِكُلِّ
شَىْءٍ عَلِيمٌ ﴿٩٧﴾ ٱعْلَمُوٓا۟ أَنَّ ٱللَّهَ شَدِيدُ ٱلْعِقَابِ وَأَنَّ ٱللَّهَ
غَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴿٩٨﴾ مَّا عَلَى ٱلرَّسُولِ إِلَّا ٱلْبَلَٰغُ ۗ وَٱللَّهُ يَعْلَمُ مَا
تُبْدُونَ وَمَا تَكْتُمُونَ ﴿٩٩﴾ قُل لَّا يَسْتَوِى ٱلْخَبِيثُ وَٱلطَّيِّبُ
وَلَوْ أَعْجَبَكَ كَثْرَةُ ٱلْخَبِيثِ ۚ فَٱتَّقُوا۟ ٱللَّهَ يَٰٓأُو۟لِى ٱلْأَلْبَٰبِ
لَعَلَّكُمْ تُفْلِحُونَ ﴿١٠٠﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ لَا تَسْـَٔلُوا۟ عَنْ
أَشْيَآءَ إِن تُبْدَ لَكُمْ تَسُؤْكُمْ وَإِن تَسْـَٔلُوا۟ عَنْهَا حِينَ يُنَزَّلُ
ٱلْقُرْءَانُ تُبْدَ لَكُمْ عَفَا ٱللَّهُ عَنْهَا ۗ وَٱللَّهُ غَفُورٌ حَلِيمٌ ﴿١٠١﴾
قَدْ سَأَلَهَا قَوْمٌ مِّن قَبْلِكُمْ ثُمَّ أَصْبَحُوا۟ بِهَا كَٰفِرِينَ ﴿١٠٢﴾ مَا جَعَلَ
ٱللَّهُ مِنۢ بَحِيرَةٍ وَلَا سَآئِبَةٍ وَلَا وَصِيلَةٍ وَلَا حَامٍ ۙ وَلَٰكِنَّ ٱلَّذِينَ
كَفَرُوا۟ يَفْتَرُونَ عَلَى ٱللَّهِ ٱلْكَذِبَ ۖ وَأَكْثَرُهُمْ لَا يَعْقِلُونَ ﴿١٠٣﴾



**(96) An halatta muku farautar dabbobin ruwa, da abin da kogi ya jeho muku, rayayye ko matacce, don amfanin wanda yake zaune a gida ko matafiyi, ya yi guzuri da shi. An haramta muku farautar tudu matuqar kuna cikin haramin hajji ko umara. Ku ji tsoron Allah ta hanyar kamanta umarninsa da nisantar haninsa. Gare shi, shi kaxai zaku koma ranar alqiyama, ya saka muku a kan ayyukanku.**
**(97) Allah ya sanya Ka'abah, xaki mai alfarma wurin tsayawar mutane, da shi ne maslahar su da addini take tsayuwa, kamar sallah, da hajji, da umara, maslaharsu ta duniya, ta samun aminci a harami, ko kawo 'ya'yan dukkan itace take samuwa. Sannan ya sanya watanni masu alfarma, waxanda su ne (Zulqa'ada, Zul-hajji, Almuharram, Rajab) suka zama wurin da suke samun aminci, ba waxanda suke yaqar su a cikinsu. Haka nan ya sanya dabbobin hadaya da abubuwan da ake rataya musu, waxanda suke nuna an koro su ne zuwa harami, su zama dalilin samun amincin ma'abotansu, ba wanda zai bijiro musu da cuta. Wannan abun da Allah ya yi muku baiwa da shi, Ya yi hakan ne don ku san Allah ya san abin da yake sama da qasa, kuma Allah ya san dukkan komai, don haka shari'arsa – wadda take kawo muku amfani, ta kawar muku da cuta, tun gabanin ta faru – tana nuna saninsa da abin da ya dace da ku.**
**(98) Yaku mutane ku sani haqiqa Allah mai tsananin uquba ne ga wanda ya sava masa. Mai yawan gafara ne ga wanda ya tuba, Mai jinqansa ne.**
**(99) Babu abin da yake kan Manzo sai isar da abin da aka umarce shi da ya isar. Ba a xora masa datar da mutane zuwa ga shiriya ba, wannan yana hannun Allah Shi kaxai. Allah ya san abin da kuke bayyanawa, da abin da kuke voyewa, na shiriya ko vata, zai kuma saka muku a kan hakan. (100) Ya kai wannan Manzo ka ce, mummuna a komai ba zai daidai da mai kyau a ba komai, koda kuwa yawan mummunan ya qayatar da kai, yawansa baya nuna falalarsa. Ku ji tsoron Allah – Ya ku masu hankali – ta hanyar barin mummuna da aikata mai kyau, ko kwa rabauta da Aljannah. (101) Ya ku waxanda suka yi imani, kada ku tambayi Manzonku abubuwan da baku da buqatarsu, ba kuma za su taimake ku a kan addininku ba, idan suka bayyana gare ku, za su munana muku, saboda wahalar dake cikinsu. Idan kuka tambayi waxannan abubuwan da aka hana ku tambaya a kansu, yayin da wahayi yake sauka ga Manzon Allah, za a bayyana muku, wannan mai sauqi ne ga Allah. Allah ya yafe abubuwa da yawa da Alqur'ani ya yi shiru a kansu, don haka kada ku yi tambaya a kansu, idan kuka yi tambaya a kansu, nauyi zai sauka a kanku na hukuncinsu. (102) Mutanen da suka gabata sun yi tambaya a kan irinsu, yayin da aka xora musu nauyi, sai suka qi aiki da su, don haka suka wayi gari suna kafirai saboda su. (103) Allah ya halatta dabbobin gida, bai haramta abin da mushirikai suka haramta wa kawunansu ba, saboda gumakansu, na Bahiira (Ita ce Taguwar da ake yanke kunneta, saboda ta haifi wani adadi na 'ya'ya). Da Saa'iba (Ita ce Taguwar da idan ta kai wasu shekaru ake qyale ta ga gumaka), da Wasiila (Ita ce Taguwar da take haihuwar mata a jere), da Hamii (Shi ne Raqumin da aka samu wasu adadi na raquma daga tsatsonsa), (duk Allah bai haramta waxannan ba) amma kafirai sun yi qarya, sun riya cewa Allah ya haramta waxannan da aka ambata. Mafi yawan kafirai ba sa bambance wa tsakanin gaskiya da qarya, da halal da haram.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:** **1 - Asalin ayyukan da Allah ya yi umarni da su, sun zo ne don tabbatar da maslahar bayi ta duniya da ta lahira, da kawar musu da cuta. 2 - Kada a ruxu da yawa, domin yawan abu ba dalili ba ne a kan halaccinsa ko daxinsa, kaxai dalili yana cikin hukuncin shari'a. 3 - Yana daga ladabin mai neman fatawa, ya qayyade tambayarsa a kan wasu iyakoki qayyadaddu. Tambayar abin da mutum baya buqatarsa, ko babu wata manufa a cikinsa bata halatta ba. 4 - Kushe hanyoyin da mushirikai suka qirqiro suka raya na haramta wasu dabbobin ni'ima, kamar Baahira, da Saa'iba, da Wasiila, da Haami.**

وَإِذَا قِيلَ لَهُمْ تَعَالَوْا۟ إِلَىٰ مَآ أَنزَلَ ٱللَّهُ وَإِلَى ٱلرَّسُولِ قَالُوا۟ حَسْبُنَا
مَا وَجَدْنَا عَلَيْهِ ءَابَآءَنَآ ۚ أَوَلَوْ كَانَ ءَابَآؤُهُمْ لَا يَعْلَمُونَ
شَيْـًٔا وَلَا يَهْتَدُونَ ﴿١٠٤﴾ يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ عَلَيْكُمْ أَنفُسَكُمْ ۖ
لَا يَضُرُّكُم مَّن ضَلَّ إِذَا ٱهْتَدَيْتُمْ ۚ إِلَى ٱللَّهِ مَرْجِعُكُمْ جَمِيعًا
فَيُنَبِّئُكُم بِمَا كُنتُمْ تَعْمَلُونَ ﴿١٠٥﴾ يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ شَهَـٰدَةُ
بَيْنِكُمْ إِذَا حَضَرَ أَحَدَكُمُ ٱلْمَوْتُ حِينَ ٱلْوَصِيَّةِ ٱثْنَانِ ذَوَا
عَدْلٍ مِّنكُمْ أَوْ ءَاخَرَانِ مِنْ غَيْرِكُمْ إِنْ أَنتُمْ ضَرَبْتُمْ فِى ٱلْأَرْضِ
فَأَصَـٰبَتْكُم مُّصِيبَةُ ٱلْمَوْتِ ۚ تَحْبِسُونَهُمَا مِنۢ بَعْدِ ٱلصَّلَوٰةِ
فَيُقْسِمَانِ بِٱللَّهِ إِنِ ٱرْتَبْتُمْ لَا نَشْتَرِى بِهِۦ ثَمَنًا وَلَوْ كَانَ ذَا
قُرْبَىٰ ۙ وَلَا نَكْتُمُ شَهَـٰدَةَ ٱللَّهِ إِنَّآ إِذًا لَّمِنَ ٱلْـَٔاثِمِينَ ﴿١٠٦﴾ فَإِنْ عُثِرَ
عَلَىٰٓ أَنَّهُمَا ٱسْتَحَقَّآ إِثْمًا فَـَٔاخَرَانِ يَقُومَانِ مَقَامَهُمَا مِنَ ٱلَّذِينَ
ٱسْتَحَقَّ عَلَيْهِمُ ٱلْأَوْلَيَـٰنِ فَيُقْسِمَانِ بِٱللَّهِ لَشَهَـٰدَتُنَآ أَحَقُّ مِن
شَهَـٰدَتِهِمَا وَمَا ٱعْتَدَيْنَآ إِنَّآ إِذًا لَّمِنَ ٱلظَّـٰلِمِينَ ﴿١٠٧﴾ ذَٰلِكَ أَدْنَىٰٓ
أَن يَأْتُوا۟ بِٱلشَّهَـٰدَةِ عَلَىٰ وَجْهِهَآ أَوْ يَخَافُوٓا۟ أَن تُرَدَّ أَيْمَـٰنٌۢ بَعْدَ
أَيْمَـٰنِهِمْ ۗ وَٱتَّقُوا۟ ٱللَّهَ وَٱسْمَعُوا۟ ۗ وَٱللَّهُ لَا يَهْدِى ٱلْقَوْمَ ٱلْفَـٰسِقِينَ ﴿١٠٨﴾



**(104) Idan aka cewa waxannan masu yi wa Allah qaryar haramta wasu dabbobin ni'ima, ku zo zuwa ga abin da Allah ya sauqar na Alqur'ani, da zuwa ga sunnar Manzon Allah (S.A.W), don ku san halal da haram, sai su ce,: "Abin da muka riqa, muka gada a wurin magabatanmu na aqidu da maganganu da ayyuka sun ishe mu". Ta yaya wannan zai ishe su, alhali magabatansu xin ba su san komai ba, kuma ba sa shiriya zuwa ga gaskiya?. Ba wanda zai bi su, sai wanda ya fisu jahilci da vacewa, su jahilai ne vatattu.**

**(105) Ya waxanda suka yi imani, ku damu da kanku, ku lazimta wa kanku yin abin da zai gyara ku, wanda ya vata daga cikin mutane, bai amsa muku ba, ba zai cutar da ku ba, in dai ku, kun shiriya. Daga cikin shiriyarku akwai umarni da kyakkyawan aiki da hana mummunan aiki da zaku yi. Ga Allah kaxai zaku koma ranar alqiyama, ya baku labarin abin da kuka kasance kuna aikatawa a duniya, kuma ya saka muku a kai.**

**(106) Ya waxanda suka yi imani, idan mutuwar xayanku ta kusanto, ta hanyar bayyanar alamomin mutuwa a jikinsa, to ya kafa shaida, ta adalai biyu daga cikin musulmai a kan wasiyyarsa, ko mutane biyu daga kafirai, idan an rasa musulmai, a yayin da kuka yi tafiya, mutuwa ta zo muku. Idan an samu kokwanto a shaidarsu, to ku tsayar da waxannan shaidu, bayan idar da xaya daga cikin sallolin farilla, su biyun su rantse da Allah, ba za su sayar da ladansu na wajen Allah da wani abu ba, ba za su ji tsoron wani makusanci ba, ba za su voye shaidar Allah dake wurinsu ba, kuma in sun aikata hakan, to sun zama masu zunubi, masu savon Allah.**

**(107) Idan bayan sun yi rantsuwa sai ya bayyana gare ku qarya suke a cikin shaidar da rantsuwar da suka yi, ko ha'incinsu ya bayyana gare ku daga baya, to sai wasu mutunen biyu, su tsaya matsayinsu, daga mafiya kusancin mutane da mamacin, su yi shaida, ko su rantse da Allah cewa shaidar da muka yi na cewa qarya suke, ko maha'inta ne ita tafi cancanta akan shaidarsu ta cewa su masu gaskiya ne da amana, kuma ba mu yi rantsuwar qarya ba. In mun yi shaidar qarya to muna cikin azzalumai, waxanda suka qetare iyakokin Allah.**

**(108) Wannan abin da aka ambata na rantsar da shaidu biyu bayan sallah, yayin da aka yi shakka a kan shaidarsu, da mayar da shaidarsu, hakan ya fi kusa da bayar da shaida a kan fuskar da ta dace da shari'a da wajen zuwa da ita, kuma ba su juyar da shaidar ba, ba za su canza ta ba, ba za su yi ha'inci ba, kuma shi ya fi kusa da su ji tsoron a mayar da rantsuwar magada bayan rantsuwarsu, sai su rantse a kan savanin abin da suka shaida da shi, sai su fallasa. Ku ji tsoron Allah ta hanyar barin qarya da ha'inci a cikin shaida da rantsuwa. Ku ji abin da aka umarce ku da shi, jin na karva. Allah baya datar da waxanda suka yi masa tawaye zuwa ga xa'arsa.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Idan bawa ya lazimta wa kansa yi wa Allah biyayya, ya yi umarni da kyakkyawan aiki, ya hana mummunan aiki, gwargwadon iyawarsa, to vatan wani ba zai cuce shi ba, kuma ba za a tambaye shi a kan wani mutum ba, musamman ma waxanda suka vata daga cikinsu.**

**2 - Kwaxaitar wa a kan rubuta wasiyya, tare da kiyaye ta, ta hanyar kafa shaidu a kanta.**

**3 - Bayanin yadda ake tambayar shaidun wasiyya a shar'ance.**

نصف الحزب ١٣

۞ يَوْمَ يَجْمَعُ ٱللَّهُ ٱلرُّسُلَ فَيَقُولُ مَاذَآ أُجِبْتُمْ ۖ قَالُوا۟ لَا عِلْمَ لَنَآ ۖ
إِنَّكَ أَنتَ عَلَّٰمُ ٱلْغُيُوبِ ﴿١٠٩﴾ إِذْ قَالَ ٱللَّهُ يَٰعِيسَى ٱبْنَ مَرْيَمَ
ٱذْكُرْ نِعْمَتِى عَلَيْكَ وَعَلَىٰ وَٰلِدَتِكَ إِذْ أَيَّدتُّكَ بِرُوحِ
ٱلْقُدُسِ تُكَلِّمُ ٱلنَّاسَ فِى ٱلْمَهْدِ وَكَهْلًا ۖ وَإِذْ عَلَّمْتُكَ
ٱلْكِتَٰبَ وَٱلْحِكْمَةَ وَٱلتَّوْرَىٰةَ وَٱلْإِنجِيلَ ۖ وَإِذْ تَخْلُقُ
مِنَ ٱلطِّينِ كَهَيْـَٔةِ ٱلطَّيْرِ بِإِذْنِى فَتَنفُخُ فِيهَا فَتَكُونُ
طَيْرًۢا بِإِذْنِى ۖ وَتُبْرِئُ ٱلْأَكْمَهَ وَٱلْأَبْرَصَ بِإِذْنِى ۖ وَإِذْ تُخْرِجُ
ٱلْمَوْتَىٰ بِإِذْنِى ۖ وَإِذْ كَفَفْتُ بَنِىٓ إِسْرَٰٓءِيلَ عَنكَ إِذْ
جِئْتَهُم بِٱلْبَيِّنَٰتِ فَقَالَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ مِنْهُمْ إِنْ هَٰذَآ
إِلَّا سِحْرٌ مُّبِينٌ ﴿١١٠﴾ وَإِذْ أَوْحَيْتُ إِلَى ٱلْحَوَارِيِّـۧنَ أَنْ ءَامِنُوا۟
بِى وَبِرَسُولِى قَالُوٓا۟ ءَامَنَّا وَٱشْهَدْ بِأَنَّنَا مُسْلِمُونَ ﴿١١١﴾
إِذْ قَالَ ٱلْحَوَارِيُّونَ يَٰعِيسَى ٱبْنَ مَرْيَمَ هَلْ يَسْتَطِيعُ رَبُّكَ
أَن يُنَزِّلَ عَلَيْنَا مَآئِدَةً مِّنَ ٱلسَّمَآءِ ۖ قَالَ ٱتَّقُوا۟ ٱللَّهَ إِن كُنتُم
مُّؤْمِنِينَ ﴿١١٢﴾ قَالُوا۟ نُرِيدُ أَن نَّأْكُلَ مِنْهَا وَتَطْمَئِنَّ قُلُوبُنَا
وَنَعْلَمَ أَن قَدْ صَدَقْتَنَا وَنَكُونَ عَلَيْهَا مِنَ ٱلشَّٰهِدِينَ ﴿١١٣﴾



**(109) Ya ku mutane ku tuna ranar alqiyama, a inda Allah zai tara dukkan Manzanni, ya ce da su: "Me al'ummunku da aka aika ku zuwa gare su, suka amsa muku da shi?". Sai su ce, suna masu mayar da amsa ga Allah: "Bamu sani ba, ilimi yana gareka ya Ubangijinmu kai kaxai. Kai ne kaxai ka san abubuwan da suke voye.**

**(110) Ka tuna lokaci da Allah ya cewa Annabi Isa (A.S): "Ya kai Isa xan Maryam, ka tuna ni'imata a kanka, lokacin da na halicce ka, ba da uba ba. Ka tuna ni'imata a kan mahaifiyarka Maryam (A.S) yayin da na zave ta a kan sauran matan zamaninta. Ka tuna daga cikin abin da na yi maka ni'ima da shi, yayin da na qarfafa ka da Mala'ika Jibrilu (A.S), kana yi wa mutane magana – alhali kana jariri – kana kiransu zuwa ga Allah, kana musu magana kana dattijo, kana faxa musu abin da na aiko ka da shi zuwa gare su. Daga cikin abin da na yi maka ni'imarsa na sanar da kai rubutu, na sanar da kai Attaura, wanda aka saukar wa Annabi Musa (A.S) da Injilar da aka saukar maka, na sanar da kai sirrikan shari'a da fa'idodinta da hikimominta. Daga cikin abin na yi maka ni'imarsa kana suranta tsuntsu daga tavo, sannan ka yi busa a cikinsa, sai ya zama tsuntsu, kana warkar da wanda aka haifa yana makaho, kana warkar da mai kuturta, fatarsa ta yi kyau, kana raya matattu ta hanyar roqon Allah a kan ya raya su, dukkan waxannan abubuwa suna faruwa ne da izini na. daga cikin ni'imar da na yi maka, Na kare ka daga Bani Isra'il, yayin da suka yi niyyar kashe ka, lokacin da ka zo musu da Mu'ujizozi bayyanannu, suka kafirce da su, suka ce: Babu abin da Isa ya zo da shi, sai sihiri bayananne".**

**(111) Ka tuna abin da na yi maka ni'imarsa, na hore maka mataimaka, yayin da na kimsawa kevantattun mabiyanka (Hawariyyun) su yi imani da ni da kai, kuma suka amsa hakan, suka ce, "Mun yi imani, ka shaida ya Ubangijinmu mu musulmi ne, masu miqa maka wuya".**

**(112) Ka tuna lokacin da Hawariyyun suka ce: "Shin Ubangijinka idan ka roqi shi zai iya saukar maka da kavaki daga sama?" Sai Annabi Isa ya amsa musu, ya umarce su da tsoron Allah, da barin wannan tambayar, domin wataqila fitina ce gare su, ya ce, ku dogara ga Ubangijinku wajen neman arziqi, in ku muminai ne".**

**(113) Sai Hawariyawa suka ce da Annabi Isa: "Muna so mu ci daga wannan kavaki ne, kuma zukatanmu su qara nutsuwa da cikar ikon Allah, da cewa kai Manzonsa ne, mu sakankance cewa ka yi mana gaskiya cikin abin da ka zo da shi, daga wajen Allah, kuma mu zama daga cikin masu shaida ga wanda bai zo ba a cikin mutane".**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Tabbatar da cewa Allah zai tara halitta a ranar alqiyama, masu darajarsu da qasqantattunsu.**

**2 - Tabbatar da Almasihu Isa xan Maryam (A.S) mutum ne, da tabbatar da ayoyinsa da Allah ya gudanar a hannunsa, waxanda ake gani, na raya matattu, da warkar da kutare da makafi.**

**3 - Bayanin da yake nuna ayoyin Annabawa suna zuwa ne don tabbatar da mabiya a kan imani, da rufe bakin waxanda suka sava, kuma waxannan ayoyin ba daga wajensu suke ba, suna zuwa ne da izinin Allah Maxaukakin Sarki.**

قَالَ عِيسَى ٱبۡنُ مَرۡيَمَ ٱللَّهُمَّ رَبَّنَآ أَنزِلۡ عَلَيۡنَا مَآئِدَةٗ مِّنَ ٱلسَّمَآءِ
تَكُونُ لَنَا عِيدٗا لِّأَوَّلِنَا وَءَاخِرِنَا وَءَايَةٗ مِّنكَۖ وَٱرۡزُقۡنَا وَأَنتَ
خَيۡرُ ٱلرَّٰزِقِينَ ١١٤ قَالَ ٱللَّهُ إِنِّي مُنَزِّلُهَا عَلَيۡكُمۡۖ فَمَن يَكۡفُرۡ بَعۡدُ
مِنكُمۡ فَإِنِّيٓ أُعَذِّبُهُۥ عَذَابٗا لَّآ أُعَذِّبُهُۥٓ أَحَدٗا مِّنَ ٱلۡعَٰلَمِينَ ١١٥
وَإِذۡ قَالَ ٱللَّهُ يَٰعِيسَى ٱبۡنَ مَرۡيَمَ ءَأَنتَ قُلۡتَ لِلنَّاسِ ٱتَّخِذُونِي
وَأُمِّيَ إِلَٰهَيۡنِ مِن دُونِ ٱللَّهِۖ قَالَ سُبۡحَٰنَكَ مَا يَكُونُ لِيٓ أَنۡ أَقُولَ
مَا لَيۡسَ لِي بِحَقٍّۚ إِن كُنتُ قُلۡتُهُۥ فَقَدۡ عَلِمۡتَهُۥۚ تَعۡلَمُ مَا فِي نَفۡسِي
وَلَآ أَعۡلَمُ مَا فِي نَفۡسِكَۚ إِنَّكَ أَنتَ عَلَّٰمُ ٱلۡغُيُوبِ ١١٦ مَا قُلۡتُ لَهُمۡ
إِلَّا مَآ أَمَرۡتَنِي بِهِۦٓ أَنِ ٱعۡبُدُواْ ٱللَّهَ رَبِّي وَرَبَّكُمۡۚ وَكُنتُ عَلَيۡهِمۡ
شَهِيدٗا مَّا دُمۡتُ فِيهِمۡۖ فَلَمَّا تَوَفَّيۡتَنِي كُنتَ أَنتَ ٱلرَّقِيبَ عَلَيۡهِمۡۚ
وَأَنتَ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ شَهِيدٌ ١١٧ إِن تُعَذِّبۡهُمۡ فَإِنَّهُمۡ عِبَادُكَۖ وَإِن
تَغۡفِرۡ لَهُمۡ فَإِنَّكَ أَنتَ ٱلۡعَزِيزُ ٱلۡحَكِيمُ ١١٨ قَالَ ٱللَّهُ هَٰذَا يَوۡمُ يَنفَعُ
ٱلصَّٰدِقِينَ صِدۡقُهُمۡۚ لَهُمۡ جَنَّٰتٞ تَجۡرِي مِن تَحۡتِهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُ خَٰلِدِينَ
فِيهَآ أَبَدٗاۖ رَّضِيَ ٱللَّهُ عَنۡهُمۡ وَرَضُواْ عَنۡهُۚ ذَٰلِكَ ٱلۡفَوۡزُ ٱلۡعَظِيمُ ١١٩ لِلَّهِ
مُلۡكُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ وَمَا فِيهِنَّۚ وَهُوَ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ قَدِيرُۢ ١٢٠



**(114) Sai Annabi Isa ya amsa musu da abin da suke nema, ya roqi Allah ya ce,: "Ya Ubangijinmu ka saukar mana da kavaki na abinci, wanda zamu riqi ranar da ya sauka ta zamar mana ranar idi, muna girmamata, don gode maka, kuma ta zama alama da hujja a kan kaxaitakarka, da gaskiyar abin da ka aiko ni da shi. Ka arzurta mu, arziqin da zai taimake mu wajen bauta maka. Kai ne – Ya Ubangijinmu – mafi alherin masu arzurtawa".**

**(115) Sai Allah ya amsa addu'ar Annabi Isa (A.S) ya ce,: "Zan saukar da wannan kavaki da kuka nemi a saukar muku, amma duk wanda ya kafirce bayan saukar da shi, to kada ya zargi kowa sai kansa, don zan azabtar da shi, azaba mai tsanani, wadda ba wanda zan yi wa irinta, saboda ya ga ayoyi masu girma, don haka kafircinsa na taurin kai ne". Allah ya cika alqawarinsa ya saukar musu da wannan kavaki.**

**(116) Ka tuna ranar alqiyama yayin da Allah zai ce - yana magana da Annabi Isa xan Maryam (A.S) -: "Ya Isa xan Maryam, shin ka faxa wa mutane: Ku mayar da ni da mahaifiyata abubuwan bauta wa koma bayan Allah?". Sai Annabi Isa ya amsa yana mai tsarkake Ubangijinsa yana mai cewa: "Bai yiwuwa gare ni, in faxa musu wani abu sai gaskiya. Kuma da za a qaddara na faxi haka, da ka sani Ya Allah, saboda babu abin da yake vuya gare ka, ka san abin da na voye a raina, amma ni ban san abin da ka voye a ranka ba. Kai kaxai ne ka san dukkan abin da baya nan, da dukkan abin da yake voye da wanda yake sarari".**

**(117) Sai Annabi Isa ya ci gaba da cewa Ubangijinsa: "Ban faxawa mutane ba, sai abin da ka umarce ni da in faxa, na umarninsu da kaxaita ka da bauta. Kuma ina kula da abin da suke faxa, tsawon zamana a cikinsu, da Ka kawo karshen zamana a cikinsu, ta hanyar xaga ni zuwa sama da raina, Ya Ubangiji kai ne mai kula da ayyukansu, kuma kai mai shaida ne a kan dukkan komai, babu abin da yake vuya gare ka, don haka abin da na faxa musu ba zai vuya gare ka ba, haka ma abin da suka faxa a bayana".**

**(118) "Ya Ubangiji idan ka azabta su, su bayinka ne, zaka aikata abin da ka ga dama da su, idan kuwa ka yi wa wanda ya yi imani a cikinsu baiwa da gafara, to babu mai hana ka, Kai ne Mabuwayi wanda ba a rinjaya, mai hikima a cikin tsare-tsarenka".**

**(119) Sai Allah ya ce wa Annabi Isa (A.S): "Wannan rana ce da masu gaskiyar niyya a cikin maganganunsu da ayyukansu, gaskiyar zata amfane su. Suna da Aljannatai waxanda qoramu suke gudana a qarqashin gine-ginensu da bishiyoyinsu, za su zauna a cikinsu har abada, ba za su mutu ba. Allah ya yarda da su, ba zai fushi da su ba, har abada, suma sun yarda da shi, saboda abin da ya same su, na ni'ima dauwamammiya. Wannan sakamako da yarda da su, shi ne babban rabo, babu wani rabo da ya kai shi.**

**(120) Allah ne kaxai yake da mulkin sammai da qassai, shi ne ya halicce su, ya tsara al'amuransu. Shi yake da mulkin abin da yake cikinsu na dukkan halitta. Kuma Shi mai iko ne a kan dukkan komai, babu abin da yake gagararsa.**

**❁ Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - Alqawarin azaba da Allah ya yi wa dukkan wanda ya zarce a kan kafirci da taurin kai, bayan hujja bayyananniya ta tsaya a gare shi. 2 - Kuvutar da Almasihu Isa xan Maryam (A.S) daga da'awar Nasara na cewa ya isar musu da saqon shi ne Allah, ko shi xan Allah ne, ko ya yi da'awar Ubangijintaka ko Allantaka. 3 - Allah Maxaukakin Sarki zai tambayi manya-manyan mutane da masu daraja daga cikin Manzanni ranar alqiyama, to yaya kuma waxanda ba su kai su ba?**
**4 - Girman matsayin gaskiya, da yabon Allah ga ma'abotanta, da bayanin amfanin gaskiya ga ma'abotanta ranar alqiyama.**

# Suratul -An'aam

An Saukar Da Ita A Makkah

## Daga Manufofin Sura:

**Tabbatar da aqidar kaxaita Allah (Wato Tauhidi) tare da hujjoji na hankali, da warware aqidun shirka.**

سُورَةُ الأَنعَامِ — آياتها ١٦٥ — ترتيبها ٦

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ
ٱلۡحَمۡدُ لِلَّهِ ٱلَّذِي خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضَ وَجَعَلَ ٱلظُّلُمَٰتِ
وَٱلنُّورَۖ ثُمَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ بِرَبِّهِمۡ يَعۡدِلُونَ ١ هُوَ ٱلَّذِي
خَلَقَكُم مِّن طِينٖ ثُمَّ قَضَىٰٓ أَجَلٗاۖ وَأَجَلٞ مُّسَمًّى عِندَهُۥۖ ثُمَّ أَنتُمۡ
تَمۡتَرُونَ ٢ وَهُوَ ٱللَّهُ فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَفِي ٱلۡأَرۡضِ يَعۡلَمُ سِرَّكُمۡ
وَجَهۡرَكُمۡ وَيَعۡلَمُ مَا تَكۡسِبُونَ ٣ وَمَا تَأۡتِيهِم مِّنۡ ءَايَةٖ مِّنۡ
ءَايَٰتِ رَبِّهِمۡ إِلَّا كَانُواْ عَنۡهَا مُعۡرِضِينَ ٤ فَقَدۡ كَذَّبُواْ بِٱلۡحَقِّ
لَمَّا جَآءَهُمۡ فَسَوۡفَ يَأۡتِيهِمۡ أَنۢبَـٰٓؤُاْ مَا كَانُواْ بِهِۦ يَسۡتَهۡزِءُونَ ٥
أَلَمۡ يَرَوۡاْ كَمۡ أَهۡلَكۡنَا مِن قَبۡلِهِم مِّن قَرۡنٖ مَّكَّنَّـٰهُمۡ فِي ٱلۡأَرۡضِ
مَا لَمۡ نُمَكِّن لَّكُمۡ وَأَرۡسَلۡنَا ٱلسَّمَآءَ عَلَيۡهِم مِّدۡرَارٗا وَجَعَلۡنَا ٱلۡأَنۡهَٰرَ
تَجۡرِي مِن تَحۡتِهِمۡ فَأَهۡلَكۡنَٰهُم بِذُنُوبِهِمۡ وَأَنشَأۡنَا مِنۢ بَعۡدِهِمۡ قَرۡنًا
ءَاخَرِينَ ٦ وَلَوۡ نَزَّلۡنَا عَلَيۡكَ كِتَٰبٗا فِي قِرۡطَاسٖ فَلَمَسُوهُ بِأَيۡدِيهِمۡ
لَقَالَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوٓاْ إِنۡ هَٰذَآ إِلَّا سِحۡرٞ مُّبِينٞ ٧ وَقَالُواْ لَوۡلَآ أُنزِلَ
عَلَيۡهِ مَلَكٞۖ وَلَوۡ أَنزَلۡنَا مَلَكٗا لَّقُضِيَ ٱلۡأَمۡرُ ثُمَّ لَا يُنظَرُونَ ٨



## Tafsir:

**(1) Siffatuwa da cikakkiyar kamala, da yabo da kyawawan abubuwa maxaukaka, tare da so, sun tabbata ga Allah, wanda ya halicci sammai da qassai, ba tare da irinsu sun gabata ba. Ya halicci dare da yini, suna bibiyar juna, dare ya halicce shi don duhu, yini kuma ya halicce shi don haske, amma duk da haka waxanda suka kafirta suke daidaita Allah da waninsa, kuma suke sanya masa abokan tarayya.**

**(2) Shi ne (Allah) tsarki ya tabbata a gare ya halicce ku – Ya ku mutane – daga tavo, yayin da ya halicci babanku Annabi Adam (A.S) daga tavon, sannan ya sanya muku ajali na tsawon zamanku a rayuwar duniya, kuma ya sanya muku wani ajalin da ba wanda ya san shi sai shi, don tashinku ranar alqiyama, amma duk da haka kuke shakka a cikin ikonsa mai girma da buwaya a kan tashinku bayan mutuwa.**

**(3) Allah (S.W.T) Shi ne abin bautawa da gaskiya a cikin sammai da qassai, babu wani abu da yake vuya a gare shi, Ya san abin da kuke voyewa na niyyoyinku da maganganunku da ayyukanku, ya kuma san abin da kuke bayyanawa daga cikin hakan, zai kuma saka muku a kan hakan.**

**(4) Ba wata hujja da zata zo wa mushirikai daga Ubangijinsu face sai sun barta, ba su damu da ita ba. To hujjoji bayyanannu da dalilai na fili sun zo muku a kan kaxaita Allah. Haka nan ayoyi masu nuna gaskiyar manzanni sun zo musu, amma duk da haka suka bijire musu, ba su damu da su ba.**

**(5) In sun bijire wa waxannan hujjoji da dalilai bayyanannu, to sun bijirewa ma abin da ya fi hakan bayyana, sun qaryata abin da Annabi Muhammad (S.A.W) ya zo da shi na Alqur'ani, kuma da sannu za su gane abin da suke izgili da shi, shi ne gaskiya, yayin da za su ga azaba, a ranar alqiyama.**

**(6) Shin waxannan kafirai ba su sani ba ne, cewa sunnar Allah ce halakar da al'ummun da suke azzalumai? Haqiqa Allah ya halakar da al'ummu masu yawa a gabaninsu, waxanda ya basu abubuwan qarfi da wanzuwa a bayan qasa, irin abin da bai ba wa waxannan kafirai ba, ya saukar musu da ruwa a jere, ya gudanar musu da qoramu suna gudana a qarqashin gidajensu, amma sai suka sava wa Allah, don haka ya halakar da su saboda abin da suka aikata na zunubi, ya halinci wasu halittun daban a bayansu.**

**(7) Ya kai wannan Manzo da mun saukar maka da littafi a rubuce a cikin takardu, suka ganshi da idanuwansu, suka tabbatar da shi, ta hanyar tava shi da hannayensu, ba za su yi imani ba, saboda jayyaya da taurin kai, kuma da sun ce: "Abin da ya zo da shi, bai wuce sihiri bayyananne ba, ba zamu yi imani da shi ba".**

**(8) Waxannan kafirai suka ce: "Ina ma Allah ya saukar da Mala'ika tare Annabi Muhammad, yana mana magana, yana shaida wa shi manzo ne, da sai mu yi imani". Da mun saukar da Mala'ika a kan siffar da suke nufi, da mun halakar da su, idan ba su yi imani ba, kuma idan Mala'ikan ya sauka ba za a jinkirta musu, su tuba ba.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Tsananin taurin kan kafirai, da bayanin zarcewarsu a kan kafirci, duk da tsayawar hujja da dalilan da ake gani ko ake ji, ko ake iya tavawa a gare su. 2 - Yin tunani a kan sunnar Allah Maxaukakin Sarki a cikin waxanda suka gabata, wajen sanin abin da ya halakar da su, don guje musu. 3 - Daga cikin rahamar Allah ga bayinsa, bai saukar musu da manzo daga cikin Mala'iku ba, saboda ba za a jinkirta musu, su tuba ba, idan Mala'ikan ya sauka.**

وَلَوۡ جَعَلۡنَٰهُ مَلَكٗا لَّجَعَلۡنَٰهُ رَجُلٗا وَلَلَبَسۡنَا عَلَيۡهِم مَّا
يَلۡبِسُونَ ٩ وَلَقَدِ ٱسۡتُهۡزِئَ بِرُسُلٖ مِّن قَبۡلِكَ فَحَاقَ بِٱلَّذِينَ
سَخِرُواْ مِنۡهُم مَّا كَانُواْ بِهِۦ يَسۡتَهۡزِءُونَ ١٠ قُلۡ سِيرُواْ
فِي ٱلۡأَرۡضِ ثُمَّ ٱنظُرُواْ كَيۡفَ كَانَ عَٰقِبَةُ ٱلۡمُكَذِّبِينَ
١١ قُل لِّمَن مَّا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۖ قُل لِّلَّهِۚ كَتَبَ عَلَىٰ
نَفۡسِهِ ٱلرَّحۡمَةَۚ لَيَجۡمَعَنَّكُمۡ إِلَىٰ يَوۡمِ ٱلۡقِيَٰمَةِ لَا رَيۡبَ
فِيهِۚ ٱلَّذِينَ خَسِرُوٓاْ أَنفُسَهُمۡ فَهُمۡ لَا يُؤۡمِنُونَ ١٢ ۞ وَلَهُۥ
مَا سَكَنَ فِي ٱلَّيۡلِ وَٱلنَّهَارِۚ وَهُوَ ٱلسَّمِيعُ ٱلۡعَلِيمُ ١٣ قُلۡ
أَغَيۡرَ ٱللَّهِ أَتَّخِذُ وَلِيّٗا فَاطِرِ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ وَهُوَ
يُطۡعِمُ وَلَا يُطۡعَمُۗ قُلۡ إِنِّيٓ أُمِرۡتُ أَنۡ أَكُونَ أَوَّلَ مَنۡ أَسۡلَمَۖ
وَلَا تَكُونَنَّ مِنَ ٱلۡمُشۡرِكِينَ ١٤ قُلۡ إِنِّيٓ أَخَافُ إِنۡ عَصَيۡتُ
رَبِّي عَذَابَ يَوۡمٍ عَظِيمٖ ١٥ مَّن يُصۡرَفۡ عَنۡهُ يَوۡمَئِذٖ فَقَدۡ رَحِمَهُۥۚ
وَذَٰلِكَ ٱلۡفَوۡزُ ٱلۡمُبِينُ ١٦ وَإِن يَمۡسَسۡكَ ٱللَّهُ بِضُرّٖ فَلَا كَاشِفَ
لَهُۥٓ إِلَّا هُوَۖ وَإِن يَمۡسَسۡكَ بِخَيۡرٖ فَهُوَ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ قَدِيرٞ
١٧ وَهُوَ ٱلۡقَاهِرُ فَوۡقَ عِبَادِهِۦۚ وَهُوَ ٱلۡحَكِيمُ ٱلۡخَبِيرُ ١٨

ثلاثة أرباع الحزب ١٣



**(9) Da mun sanya wanda muka aiko musu ya zama Mala'ika, to da mun mayar da shi a kamannin mutum, saboda su samu damar sauraransa da karvar abin da ya zo da shi, domin ba za su iya hakan da Mala'ika ba, idan yana kan kamanninsa, idan kuma muka sanya shi a kamannin mutum da lamarin ya cakuxe musu.**

**(10) Idan waxannan sun maka izgili da neman a saukar da Mala'ika a tare da kai, to tabbas al'ummun da suka gabata sun yi izgili ga Manzanninsu, sai azabar da suke qaryata wa, suke izgili da ita ta kewaye su.**

**(11) Ya kai wannan Manzo ka ce wa waxannan masu qaryata wa da izgili: "ku tafi a bayan qasa, sannan ku lura yaya qarshen masu qaryata Manzanni yake kasancewa?. Azaba ta sauka a kansu, bayan da suna cikin kariya da qarfi.**

**(12) Ka ce da su ya kai wannan Manzo, Mulkin sammai da qassai da abin da yake tsakaninsu, na waye? Ka ce: "Mulkinsu na Allah ne, ya wajabta wa kansa rahama, saboda falala ga bayinsa, ba ya gaggauta musu azaba, har sai idan ba su tuba ba zai tara su zuwa ranar alqiyama, ranar da babu shakka a cikinta. Waxanda suka yi hasarar kawunansu, ta hanyar kafirci ba sa yin imani, balle su ceci kansu daga tavewa.**

**(13) Allah ne kaxai Mamallakin dukkan komai, abin da yake cikin dare da yini. Shi ne mai jin maganganu, Masani da ayyukan bayi, kuma zai saka musu a kansu.**

**(14) Ya kai wannan Annabi, ka cewa mushirikai waxanda suke bauta wa Allah tare da wani abu daga cikin gumaka: "Yanzu zai yi wu a hankali in riqi wanin Allah a matsayin mataimaki, ina neman taimakonsa? Alhali Allah, shi ne ya halicci sammai da qassai, ba tare da ya ga samfur a wurin wani ba, ba wanda ya riga shi halittar irinsu. Kuma shi ne yake arzurta wanda ya ga dama daga cikin bayinsa, babu wani daga cikin bayinsa da yake arzurta wa, kuma shi ne Mawadaci daga bayinsa, bayinsa mabuqata ne gare shi". Ka ce da su – ya kai wannan manzo –: "Haqiqa Allah ya umarce ni, in kasance farkon wanda ya miqa wuya, ya qanqan da kai a cikin wannan al'umma, Ya hana ni in kasance cikin waxanda suke haxa shi da wani a wajen bauta (wato shirka)".**

**(15) Ya kai wannan Manzo ka ce,: "Haqiqa ni ina jin tsoro in na sava wa Allah, ta hanyar aikata abin da ya haramta min na shirka da waninta, ko na bar abin ya umarce ni da shi, na imani da sauran ayyukan xa'a. ina tsoron ya azabta ni azaba mai girma ranar alqiyama". (16) Wanda Allah ya nisantar masa da wannan azabar ta ranar alqiyama, to ya rabauta da rahamar Allah gare shi. Wannan tsiran kuwa shi ne rabo mabayyani, wanda babu rabon da ya kai shi. (17) Ya kai xan adam idan bala'i ya shafe ka daga wajen Allah, babu mai kare ka daga gare shi sai Allah. Idan alheri ya same ka daga gare shi, babu mai hana hakan, babu mai mayar da falalarsa, kuma shi ne mai iko a kan dukkan komai, babu abin da yake gagararsa.**

**(18) Shi ne mai rinjaye a kan bayinsa, masu qasqanta gare shi, shi kuma maxaukaki a kansu, ta kowace fuska, babu abin da yake gagararsa, babu wanda yake rinjayarsa, kowa da kowa ya qasqanta gare shi. Yana saman bayinsa, yadda ya dace da shi (S.W.T). Shi ne mai hikima a cikin halittarsa da tsarinsa, da shari'arsa. Kuma shi ne masani mai bada labari, babu abin da yake vuya gare shi.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - Bayanin hikimar Allah a cikin aiko da kowane manzo daga jinsin waxanda ya aiko musu da manzon, saboda su kai matuqa wajen sauraro da kiyayewa, da karvar abin da ya zo da shi. 2 - Kira zuwa ga lura da cewa maimaita sunnar mutanen farko wajen savo, yana kawo maimaituwar sunnar Allah Maxaukakin Sarki a wajen uquba. 3 - Abin da yake samun mutum na bala'i, babu mai kawar da shi sai Allah, abin da yake samun sa na alheri, babu mai hana shi, sai Allah, babu mai mayar da falalarsa, babu mai kare ni'imarsa.**

قُلْ أَيُّ شَيْءٍ أَكْبَرُ شَهَٰدَةً ۖ قُلِ ٱللَّهُ ۖ شَهِيدٌۢ بَيْنِى وَبَيْنَكُمْ ۚ وَأُوحِىَ إِلَىَّ هَٰذَا
ٱلْقُرْءَانُ لِأُنذِرَكُم بِهِۦ وَمَنۢ بَلَغَ ۚ أَئِنَّكُمْ لَتَشْهَدُونَ أَنَّ مَعَ ٱللَّهِ ءَالِهَةً
أُخْرَىٰ ۚ قُل لَّآ أَشْهَدُ ۚ قُلْ إِنَّمَا هُوَ إِلَٰهٌ وَٰحِدٌ وَإِنَّنِى بَرِىٓءٌ مِّمَّا تُشْرِكُونَ
﴿١٩﴾ ٱلَّذِينَ ءَاتَيْنَٰهُمُ ٱلْكِتَٰبَ يَعْرِفُونَهُۥ كَمَا يَعْرِفُونَ أَبْنَآءَهُمُ ۘ ٱلَّذِينَ
خَسِرُوٓا۟ أَنفُسَهُمْ فَهُمْ لَا يُؤْمِنُونَ ﴿٢٠﴾ وَمَنْ أَظْلَمُ مِمَّنِ ٱفْتَرَىٰ عَلَى
ٱللَّهِ كَذِبًا أَوْ كَذَّبَ بِـَٔايَٰتِهِۦٓ ۗ إِنَّهُۥ لَا يُفْلِحُ ٱلظَّٰلِمُونَ ﴿٢١﴾ وَيَوْمَ نَحْشُرُهُمْ
جَمِيعًا ثُمَّ نَقُولُ لِلَّذِينَ أَشْرَكُوٓا۟ أَيْنَ شُرَكَآؤُكُمُ ٱلَّذِينَ كُنتُمْ تَزْعُمُونَ ﴿٢٢﴾
ثُمَّ لَمْ تَكُن فِتْنَتُهُمْ إِلَّآ أَن قَالُوا۟ وَٱللَّهِ رَبِّنَا مَا كُنَّا مُشْرِكِينَ ﴿٢٣﴾
ٱنظُرْ كَيْفَ كَذَبُوا۟ عَلَىٰٓ أَنفُسِهِمْ ۚ وَضَلَّ عَنْهُم مَّا كَانُوا۟ يَفْتَرُونَ ﴿٢٤﴾
وَمِنْهُم مَّن يَسْتَمِعُ إِلَيْكَ ۖ وَجَعَلْنَا عَلَىٰ قُلُوبِهِمْ أَكِنَّةً أَن يَفْقَهُوهُ
وَفِىٓ ءَاذَانِهِمْ وَقْرًا ۚ وَإِن يَرَوْا۟ كُلَّ ءَايَةٍ لَّا يُؤْمِنُوا۟ بِهَا ۚ حَتَّىٰٓ إِذَا
جَآءُوكَ يُجَٰدِلُونَكَ يَقُولُ ٱلَّذِينَ كَفَرُوٓا۟ إِنْ هَٰذَآ إِلَّآ أَسَٰطِيرُ
ٱلْأَوَّلِينَ ﴿٢٥﴾ وَهُمْ يَنْهَوْنَ عَنْهُ وَيَنْـَٔوْنَ عَنْهُ ۖ وَإِن يُهْلِكُونَ إِلَّآ
أَنفُسَهُمْ وَمَا يَشْعُرُونَ ﴿٢٦﴾ وَلَوْ تَرَىٰٓ إِذْ وُقِفُوا۟ عَلَى ٱلنَّارِ فَقَالُوا۟
يَٰلَيْتَنَا نُرَدُّ وَلَا نُكَذِّبَ بِـَٔايَٰتِ رَبِّنَا وَنَكُونَ مِنَ ٱلْمُؤْمِنِينَ ﴿٢٧﴾



**(19) Ya kai wannan Manzo ka ce wa mushirikai waxanda suke qaryata ka: "Wane abu ne yafi girma da xaukaka a kan shaidawa da gaskiya ta?" Ka ce, "Allah ne mafi girma da xaukaka a wajen shaida wa da gaskiyata. Shi ne shaida tsakanina da ku, ya san abin da na zo muku da shi, da abin da zaku bani amsa da shi. Haqiqa Allah ya yi min wahayin wannan Alqur'ani don in tsoratar da ku da shi, in tsoratar da wanda ya isa gare shi, daga aljannu da mutane. Haqiqa ku waxannan mushirikai kun yi imani akwai wasu abubuwan bauta tare da Allah". Ka ce musu – Ya kai wannan Manzo – "Ni bana shaida wa da abin da, ku da kanku kun tabbatar da vacinsa. Allah ne kaxai abin bautawa, Shi kaxai, ba shi da abokin tarayya, kuma na barranta daga dukkan abin da kuke shirka da shi".**

**(20) Yahudawan da muka ba su Attaura da Nasara da muka ba su Injila, sun san Annabi Muhammad sani cikakke, kamar yadda suke bambance 'ya'yansu daga 'ya'yan wasunsu, to waxannan sun yi asarar kawunansu da shigar da su wuta, don ba su yi imani ba.**

**(21) Ba wanda ya fi girman zalunci fiye da wanda ya dangana wa Allah abokin tarayya, ya bauta masa tare da wani, ko ya qaryata ayoyinsa waxanda ya saukar da su ga Manzonsa. Waxanda suka yi zalunci ta hanyar dangana wa Allah abokin tarayya da qaryata ayoyinsa ba sa rabauta har abada, in ba su tuba ba.**

**(22) Ka tuna ranar alqiyama yayin da zamu tara su gaba xaya, ba wanda zamu bari, sannan mu cewa waxanda suka bautawa wani tare da Allah, muna masu wulaqanta su: "Ina abokan tarayyar naku, waxanda kuke qaryar cewa su abokan tarayyar Allah ne?".**

**(23) Sannan ba su da wani uzuri bayan wannan jarrabawar, sai dai su barranta daga abubuwan bautarsu. Suka yi qarya suka ce, "Wallahi ya Ubangijinmu, mu a duniya bama yin shirka da kai, mun kasance masu imani da kai, masu kaxaitaka". (24) Ka duba – Ya kai wannan manzo – yadda waxannan suka yi wa kansu qarya, ta hanyar kore wa kansu shirka. Sannan abubuwan da suka qirqiro na abokan tarayya ga Allah a duniya suka vace musu, suka qasqanta su?!".**

**(25) Ya kai wannan manzo, daga cikin mushirikai akwai masu sauraronka idan kana karanta Al'qur'ani, sai dai ba sa amfanuwa da abin da suke saurare daga gareka, saboda mun sa rufi a kan zukatansu, don kada su fahimci Alqur'ani, saboda girman kansu da bijirewarsu. Mun sanya kurumta a cikin kunnuwansu, ba sa ji mai amfani. Duk irin yadda suka ga ayoyi bayyanannu da hujjoji ba za su yi imani da su ba, har idan sun zo wajenka suna jayayya da kai, da varna a kan gaskiya, sai su riqa cewa: "Ba abin da ka zo da shi, face abin da ka samo daga littafan mutanen farko".**

**(26) Suna hana mutane imani da Manzo, kuma suna nisantarsa, ba sa barin wanda zai amfanu da shi, su kuma ba sa amfana da shi, amma ba kowa suke halakarwa ba face kawunansu, kuma ba su san abin da suke aikatawa halakar da ita ne ba. (27) Ya kai wannan manzo, da zaka ga yayin da ake bijirar da su ga wuta ranar alqiyama, suna cewa cikin nadama: "Kaiconmu! Ina ma za a mayar da mu rayuwar duniya, ba za mu qaryata ayoyin Allah ba, kuma mu zama daga cikin wadanda suka yi imani da Allah". Da zaka ga haka, da ka ga abin mamaki, saboda yadda halin da suke ciki ya yi muni.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - Bayanin hikimar aiko Annabi (S.A.W) da Alqur'ani, don isarwa ne da bayani, kuma mafi girman hakan shi ne kaxaita Allah (Tauhid). 2 - Korewa Allah abokin tarayya, da bice qarairayin mushirikai a wannan vangare. 3 - Bayanin cewa Yahudawa da Nasara sun san Annabi (S.A.W), duk da kafircinsu da jayayyarsu.**

بَلۡ بَدَا لَهُم مَّا كَانُواْ يُخۡفُونَ مِن قَبۡلُۖ وَلَوۡ رُدُّواْ لَعَادُواْ لِمَا نُهُواْ عَنۡهُ
وَإِنَّهُمۡ لَكَٰذِبُونَ ٢٨ وَقَالُوٓاْ إِنۡ هِيَ إِلَّا حَيَاتُنَا ٱلدُّنۡيَا وَمَا نَحۡنُ
بِمَبۡعُوثِينَ ٢٩ وَلَوۡ تَرَىٰٓ إِذۡ وُقِفُواْ عَلَىٰ رَبِّهِمۡۚ قَالَ أَلَيۡسَ هَٰذَا
بِٱلۡحَقِّۚ قَالُواْ بَلَىٰ وَرَبِّنَاۚ قَالَ فَذُوقُواْ ٱلۡعَذَابَ بِمَا كُنتُمۡ تَكۡفُرُونَ
٣٠ قَدۡ خَسِرَ ٱلَّذِينَ كَذَّبُواْ بِلِقَآءِ ٱللَّهِۖ حَتَّىٰٓ إِذَا جَآءَتۡهُمُ ٱلسَّاعَةُ
بَغۡتَةٗ قَالُواْ يَٰحَسۡرَتَنَا عَلَىٰ مَا فَرَّطۡنَا فِيهَا وَهُمۡ يَحۡمِلُونَ أَوۡزَارَهُمۡ
عَلَىٰ ظُهُورِهِمۡۚ أَلَا سَآءَ مَا يَزِرُونَ ٣١ وَمَا ٱلۡحَيَوٰةُ ٱلدُّنۡيَآ
إِلَّا لَعِبٞ وَلَهۡوٞۖ وَلَلدَّارُ ٱلۡأٓخِرَةُ خَيۡرٞ لِّلَّذِينَ يَتَّقُونَۚ أَفَلَا تَعۡقِلُونَ
٣٢ قَدۡ نَعۡلَمُ إِنَّهُۥ لَيَحۡزُنُكَ ٱلَّذِي يَقُولُونَۖ فَإِنَّهُمۡ لَا يُكَذِّبُونَكَ
وَلَٰكِنَّ ٱلظَّٰلِمِينَ بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ يَجۡحَدُونَ ٣٣ وَلَقَدۡ كُذِّبَتۡ
رُسُلٞ مِّن قَبۡلِكَ فَصَبَرُواْ عَلَىٰ مَا كُذِّبُواْ وَأُوذُواْ حَتَّىٰٓ أَتَىٰهُمۡ
نَصۡرُنَاۚ وَلَا مُبَدِّلَ لِكَلِمَٰتِ ٱللَّهِۚ وَلَقَدۡ جَآءَكَ مِن نَّبَإِيْ ٱلۡمُرۡسَلِينَ
٣٤ وَإِن كَانَ كَبُرَ عَلَيۡكَ إِعۡرَاضُهُمۡ فَإِنِ ٱسۡتَطَعۡتَ أَن تَبۡتَغِيَ
نَفَقٗا فِي ٱلۡأَرۡضِ أَوۡ سُلَّمٗا فِي ٱلسَّمَآءِ فَتَأۡتِيَهُم بِـَٔايَةٖۚ وَلَوۡ شَآءَ
ٱللَّهُ لَجَمَعَهُمۡ عَلَى ٱلۡهُدَىٰۚ فَلَا تَكُونَنَّ مِنَ ٱلۡجَٰهِلِينَ ٣٥



**(28) Lamarin ba kamar yadda suka ce ba ne, cewa da an mayar da su, da sun yi imani, kawai dai abin da suke voye wa ne na cewar su (Wallahi bamu kasance masu yin shirka ba) ya bayyana gare su, yayin da gavvansu suka bada shaida a kansu. Da za a qaddara sun dawo duniya, da sun koma zuwa ga abin da aka hana na kafirci da shirka, kuma haqiqa su qarya suke cikin alqawarinsu na yin imani idan sun dawo.**

**(29) Waxannan mushirikai suka ce,: "Ba wata rayuwa sai rayuwar da muke cikinta a yanzu, kuma ba za a tashe mu don yin hisabi ba".**

**(30) Ya kai wannan Manzo da zaka ga yayin da aka tsayar da masu inkarin tashi bayan mutuwa a gaban Ubangijinsu, da ka ga abin mamaki, saboda mummunan halin da suke ciki, a lokacin da Allah zai ce musu: "Yanzu wannan tashin da aka yi bayan mutuwa, wanda kuke qaryata wa ba gaskiya ba ne, tabbatacce, wanda babu shakka a cikinsa?" Sai suka ce,: "Mun rantse da Ubangijinmu wanda ya halicce mu, tabbas gaskiya ne, babu shakka a cikinsa". Sai Allah ya ce da su a wannan lokacin: "Ku xanxani azaba saboda kafirce wa wannan rana da kuka yi, da qaryata wa da ita a rayuwarku ta duniya".**

**(31) Tabbas waxanda suka qaryata da tashi ranar alqiyama, suka nisantar da tsayawa gaban Allah sun yi hasara. Har sai alqiyama ta zo musu kwatsam, ba tare da sun sani ba, sai su ce a cikin tsananin nadama: "Ya hasaranmu da tavewarmu saboda gazawarmu a vangaren Allah, na kafirce wa da shi, da rashin shirin zuwan wannan rana ta alqiyama!", suna xauke da munanan ayyukansu a bayansu. Ku saurara! Abin da suke xauke da shi na munanan ayyuka ya yi muni. (32) Wannan rayuwar duniyar da kuke karkata zuwa gare ta, ba komai ba ce face wasa da ruxi, ga wanda bai yi aikin da Allah ya yarda da shi ba. Amma gidan lahira shi ne ya fi alheri ga waxanda suke tsoron Allah, ta hanyar aikata abin da ya yi umarni da shi na imani da biyayya, da barin abin da ya hana na shirka da savo. Yanzu ba za ku hankalta da haka ba, ya ku waxannan mushirikai! Ku yi imani ku aikata ayyuka nagartattu. (33) Ya kai wannan Manzo, Mun sani kana baqin ciki da qaryatawar da suke yi maka a zahiri, to ka sani, su basa qaryata ka a cikin zukatansu, saboda sun san gaskiyarka da amanarka, kwai dai su mutane ne azzalumai, suna inkarin lamarinka ne a zahiri, amma kuma a zukatansu suna masu yaqini da shi. (34) Kada ka xauka wannan qaryatawar ta kevanta ne da abin da ka zo da shi. Haqiqa an qaryata wasu manzanni gabaninka, mutanensu sun cutar da su, amma sai suka fuskanci haka da haquri a wajen kira, da jihadi a kan tafarkin Allah, har nasara daga wajen Allah ta zo musu, babu mai canza abin da Allah ya rubuta na nasara, wadda ya yi wa manzanninsa alqawari da ita. Haqiqa – ya kai wannan Manzo – labarun manzannin da suka gabace ka ya zo maka, da abin da suka gamu da shi daga wurin mutanensu, da abin da Allah ya ba su na nasara a kan maqiyansu ta hanyar halakar da su. (35) Ya kai wannan Manzo idan abin da kake gamuwa da shi na qaryatawarsu da bijirewarsu daga abin da ka zo musu da shi na gaskiya, yana maka tsananani, to in zaka iya neman wata mashiga a bayan qasa, ko abin hawa zuwa sama, don ka zo musu da wata hujja da wani dalili, ba wanda muka qarfafa ka da shi ba, to ka yi hakan. Da Allah ya ga damar ya haxa su a kan shiriyar da ka zo da ita, da ya haxa su, sai dai bai ga damar hakan ba, saboda wata babbar hikima, don haka kada ka zama cikin waxanda suka jahilci hakan, zuciyarka ta qare wajen damuwa a kan ba su yi imani ba.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - Saboda adalcin Allah Maxaukakin Sarki zai tara mai bauta da wanda ake bauta wa, mabiyi da wanda ake bi, a filin alqiyama, don sashensu ya yi wa sashe shaida. 2 - Ba duk wanda yake jin Alqur'ani ne yake amfana da shi ba, za a iya samun wani abin da zai hana amfanuwa da shi, kamar rufin zukata, kurumta, da sauransu. 3 - Bayanin cewa mushirikai duk da suna qaryata Manzon Allah a zahiri, to amma fa suna da yaqini a zukatansu na gaskiyar Manzon Allah (S.A.W) xin.**

**4 - Lallashin Annabi (S.A.W) da ba shi haquri da sanar da shi cewa wannan qaryatawar ba gare shi kaxai ta faru ba, a'a, al'adar mushirikai ce wajen mu'amalatar Manzannin da suka gabata.**

الحزب ١٤

۞ إِنَّمَا يَسْتَجِيبُ ٱلَّذِينَ يَسْمَعُونَ ۘ وَٱلْمَوْتَىٰ يَبْعَثُهُمُ ٱللَّهُ ثُمَّ إِلَيْهِ
يُرْجَعُونَ ﴿٣٦﴾ وَقَالُوا۟ لَوْلَا نُزِّلَ عَلَيْهِ ءَايَةٌ مِّن رَّبِّهِۦ ۚ قُلْ إِنَّ ٱللَّهَ
قَادِرٌ عَلَىٰٓ أَن يُنَزِّلَ ءَايَةً وَلَـٰكِنَّ أَكْثَرَهُمْ لَا يَعْلَمُونَ ﴿٣٧﴾ وَمَا
مِن دَآبَّةٍ فِى ٱلْأَرْضِ وَلَا طَـٰٓئِرٍ يَطِيرُ بِجَنَاحَيْهِ إِلَّآ أُمَمٌ أَمْثَالُكُم ۚ
مَّا فَرَّطْنَا فِى ٱلْكِتَـٰبِ مِن شَىْءٍ ۚ ثُمَّ إِلَىٰ رَبِّهِمْ يُحْشَرُونَ ﴿٣٨﴾
وَٱلَّذِينَ كَذَّبُوا۟ بِـَٔايَـٰتِنَا صُمٌّ وَبُكْمٌ فِى ٱلظُّلُمَـٰتِ ۗ مَن يَشَإِ
ٱللَّهُ يُضْلِلْهُ وَمَن يَشَأْ يَجْعَلْهُ عَلَىٰ صِرَٰطٍ مُّسْتَقِيمٍ ﴿٣٩﴾ قُلْ
أَرَءَيْتَكُمْ إِنْ أَتَىٰكُمْ عَذَابُ ٱللَّهِ أَوْ أَتَتْكُمُ ٱلسَّاعَةُ أَغَيْرَ ٱللَّهِ
تَدْعُونَ إِن كُنتُمْ صَـٰدِقِينَ ﴿٤٠﴾ بَلْ إِيَّاهُ تَدْعُونَ فَيَكْشِفُ
مَا تَدْعُونَ إِلَيْهِ إِن شَآءَ وَتَنسَوْنَ مَا تُشْرِكُونَ ﴿٤١﴾ وَلَقَدْ أَرْسَلْنَآ
إِلَىٰٓ أُمَمٍ مِّن قَبْلِكَ فَأَخَذْنَـٰهُم بِٱلْبَأْسَآءِ وَٱلضَّرَّآءِ لَعَلَّهُمْ
يَتَضَرَّعُونَ ﴿٤٢﴾ فَلَوْلَآ إِذْ جَآءَهُم بَأْسُنَا تَضَرَّعُوا۟ وَلَـٰكِن قَسَتْ
قُلُوبُهُمْ وَزَيَّنَ لَهُمُ ٱلشَّيْطَـٰنُ مَا كَانُوا۟ يَعْمَلُونَ ﴿٤٣﴾ فَلَمَّا
نَسُوا۟ مَا ذُكِّرُوا۟ بِهِۦ فَتَحْنَا عَلَيْهِمْ أَبْوَٰبَ كُلِّ شَىْءٍ حَتَّىٰٓ
إِذَا فَرِحُوا۟ بِمَآ أُوتُوٓا۟ أَخَذْنَـٰهُم بَغْتَةً فَإِذَا هُم مُّبْلِسُونَ ﴿٤٤﴾



**(36) Kaxai waxanda suke amsa maka, sune waxanda suke jin zance, kuma suke fahimtarsa. Amma kafirai matattu ne, ba su da wani sha'ani, zukatansu sun mutu. Matattu kuwa Allah zai tashe su ranar alqiyama ne, sannan gare shi, shi kaxai za su koma, don ya saka musu a kan abin da suka gabatar.**

**(37) Mushirikai suka ce, suna masu taurin kai da jan-qafa wajen imani: "Ina ma an saukar wa da Muhammadu wata aya, da ta savawa al'ada, don ta zama hujja daga Ubangijinsa a kan gaskiyar abin da ya zo da shi?". Ka ce – ya kai wannan Manzo –: "Haqiqa Allah yana da ikon saukar da aya kamar yadda suke so, sai dai mafi yawan mushirikai, masu neman saukar da aya, basu san cewa saukar da ayoyi yana kasancewa daidai da hikimar Allah ba, ba daidai da yadda suke so ba". Kuma da ya saukar da ita, sannan suka qi imani, to da ya halakar da su.**

**(38) Babu wata dabba da take motsi a bayan qasa, ko tsuntsu da yake tashi a sama, face jinsi-jinsi ne irinku – Ku 'Yan adam – a wajen halitta da arziqi. Babu abin da muka bari a Lauhul Mahfuzu face sai mun tabbatar da shi. Sanin dukkaninsu yana wajen Allah, sannan zuwa ga Ubangijinsu kaxai ranar alqiyama, za a tara su don yanke musu hukunci, ya sakawa kowa da abin da ya dace da shi.**

**(39) Waxanda suka qaryata da ayoyinmu, kamar kurame ne waxanda ba sa ji, da bebayen da ba sa magana, kuma suna cikin duhu ba sa gani, to ta yaya wanda yake cikin wannan hali zai shiriya?!. Wanda Allah ya ga damar vatar da shi, sai ya vatar da shi. Wanda ya ga damar shiriyarsa, sai ya shirye shi, ya sanya shi a kan tafarki madaidaici, wanda babu karkata a cikinsa. (40) Ya kai wannan Manzo ka cewa waxannan mushirikai: "Ku bani labari in azaba ta zo muku daga wajen Allah, ko alqiyamar da aka yi muku alqawarinta ta zo muku, zaku nemi wanin Allah ne a lokacin, don ya yaye muku abin da ya sauka a kanku na bala'i da tsanani, in dai da gaskiya kuke a cikin da'awarku na abubuwan bautarku suna jawo amfani ko suna kawar da cuta?!!.**

**(41) Alal-haqiqa a lokacin ba wanda zaku kira sai Allah da ya halicce ku, ya kawar muku da bala'i, ya xauke muku cuta, Shi ne majivincin haka, kuma mai iko a kai. Amma abubuwan bautarku waxanda kuke haxa Allah da su, sai ku bar su, saboda kun san ba sa amfanarwa ko cutarwa.**

**(42) Haqiqa mun aika Manzanni zuwa ga al'ummun da suke gabaninka, sai suka qaryata su, suka bijire wa abin da suka zo da shi, sai muka yi musu uquba da tsanani, kamar talauci da abin da zai cutar da jikinsu, kamar rashin lafiya, saboda su qasqantar da kai ga Ubangijinsu, su koma gare shi.**

**(43) Da a ce yayin da bala'inmu ya same su, sun qasqantar da kai ga Allah, sun sunkuya gare shi, don ya yaye musu bala'i, da mun jiqan su, amma ba su aikata haka ba, zukatansu sun qeqeshe, ba su xau izina ba, ba su wa'azantu ba. Kuma Shaixan ya kyautata musu abin da suke kai na kafirci da savo, suka ci gaba a kan abin da suke kai.**

**(44) Da suka bar abin da aka yi musu wa'azi da shi, na tsananin talauci da rashin lafiya, ba su yi aiki da umarnin Allah ba, sai muka yi musu talala, ta hanyar buxe qofofin arziki da wadata gare su, bayan talauci, muka basu lafiya a jikinsu, bayan rashin lafiya, har sai da suka yi girman kai, suka yi ji-ji-da-kai da abin da aka jiyar da su na daxi sai azaba ta zo musu kwatsam, sai ga su, sun ruxe, sun xebe qauna daga abin da suke buri.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Kamanta kafirai da matattu, saboda rayuwa ta haqiqa ita ce rayuwar zukata, ta hanyar karvar gaskiya da bin tafarkin shiriya. 2 - Daga cikin hikimar Allah a cikin jarrabawar da yake wa bayinsa, akwai saukar da bala'i ga waxanda suka sava, saboda zukatansu su yi laushi, su koma zuwa ga Ubangijinsu. 3 - Samuwar ni'ima da dukiya a hannun vatattu baya nuna son Allah gare su, kaxai hakan talala ce da jarrabawa gare su da waninsu.**

فَقُطِعَ دَابِرُ ٱلۡقَوۡمِ ٱلَّذِينَ ظَلَمُواْۚ وَٱلۡحَمۡدُ لِلَّهِ رَبِّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ٤٥
قُلۡ أَرَءَيۡتُمۡ إِنۡ أَخَذَ ٱللَّهُ سَمۡعَكُمۡ وَأَبۡصَٰرَكُمۡ وَخَتَمَ عَلَىٰ قُلُوبِكُم
مَّنۡ إِلَٰهٌ غَيۡرُ ٱللَّهِ يَأۡتِيكُم بِهِۗ ٱنظُرۡ كَيۡفَ نُصَرِّفُ ٱلۡأٓيَٰتِ
ثُمَّ هُمۡ يَصۡدِفُونَ ٤٦ قُلۡ أَرَءَيۡتَكُمۡ إِنۡ أَتَىٰكُمۡ عَذَابُ ٱللَّهِ
بَغۡتَةً أَوۡ جَهۡرَةً هَلۡ يُهۡلَكُ إِلَّا ٱلۡقَوۡمُ ٱلظَّٰلِمُونَ ٤٧ وَمَا
نُرۡسِلُ ٱلۡمُرۡسَلِينَ إِلَّا مُبَشِّرِينَ وَمُنذِرِينَۖ فَمَنۡ ءَامَنَ وَأَصۡلَحَ
فَلَا خَوۡفٌ عَلَيۡهِمۡ وَلَا هُمۡ يَحۡزَنُونَ ٤٨ وَٱلَّذِينَ كَذَّبُواْ بِـَٔايَٰتِنَا
يَمَسُّهُمُ ٱلۡعَذَابُ بِمَا كَانُواْ يَفۡسُقُونَ ٤٩ قُل لَّآ أَقُولُ لَكُمۡ
عِندِي خَزَآئِنُ ٱللَّهِ وَلَآ أَعۡلَمُ ٱلۡغَيۡبَ وَلَآ أَقُولُ لَكُمۡ إِنِّي مَلَكٌۖ
إِنۡ أَتَّبِعُ إِلَّا مَا يُوحَىٰٓ إِلَيَّۚ قُلۡ هَلۡ يَسۡتَوِي ٱلۡأَعۡمَىٰ وَٱلۡبَصِيرُۚ
أَفَلَا تَتَفَكَّرُونَ ٥٠ وَأَنذِرۡ بِهِ ٱلَّذِينَ يَخَافُونَ أَن يُحۡشَرُوٓاْ إِلَىٰ
رَبِّهِمۡ لَيۡسَ لَهُم مِّن دُونِهِۦ وَلِيّٞ وَلَا شَفِيعٞ لَّعَلَّهُمۡ يَتَّقُونَ
٥١ وَلَا تَطۡرُدِ ٱلَّذِينَ يَدۡعُونَ رَبَّهُم بِٱلۡغَدَوٰةِ وَٱلۡعَشِيِّ يُرِيدُونَ
وَجۡهَهُۥۖ مَا عَلَيۡكَ مِنۡ حِسَابِهِم مِّن شَيۡءٖ وَمَا مِنۡ حِسَابِكَ
عَلَيۡهِم مِّن شَيۡءٖ فَتَطۡرُدَهُمۡ فَتَكُونَ مِنَ ٱلظَّٰلِمِينَ ٥٢



**45 Sai aka yanke qarshen waxanda suka yi kafirci, ta hanyar tunvuke su da halakar da su gaba xaya, da ba wa Manzannin Allah nasara. Godiya da yabo sun tabbata ga Allah shi kaxai, Ubangijin talikai, a kan halakar da maqiyansa da taimakon masoyansa.**

**46 Ka cewa mushirikai – ya kai wannan Manzo –: “Ku bani labari, idan Allah ya kurumtar da ku, ya janye jin ku, ya makantar da ku, ya karve ganinku, ya rufe zukatanku, bakwa fahimtar komai, wane abin bauta wa ne na gaskiya da zai zo muku da abin da kuka rasa?”. Ka lura – ya kai wannan Manzo – yaya muke bayyana musu hujjoji, muke cancanza musu dalilai, sannan su, suna bijire musu.**

**47 Ka ce – ya kai wannan Manzo –: “ku bani labari idan azabar Allah ta zo muku ba shiri, ba tare da saninku ba, ko ta zo muku a fili ido-da-ido, ba wanda za a kama da wannan azaba sai azzalumai, saboda kafirce wa Allah da qaryata manzanninsa”.**

**48 Ba mu aika wanxanda muka aika daga Manzanninmu da komai ba, sai don ba wa masu imani da biyayya labarin da zai faranta musu, na ni’ima dauwamammiya, wadda ba ta qarewa, ba ta yankewa, da kuma tsoratar da kafirai da masu savo daga azabarmu mai tsanani. Duk wanda ya yi imani da Manzanni, ya gyara aikinsa, to babu tsoro a kansu cikin abin da suke fuskanta a lahira, kuma ba za su yi baqin ciki da nadama a kan abin da ya wuce su, na rabon duniya ba.**

**49 Waxanda suka qaryata ayoyinmu azaba zata same su, saboda fitarsu daga xa’ar Allah.**

**50 Ka cewa waxannan mushirikai – ya kai wannan Manzo –: “Ba zan ce da ku ni ina da taskokin Allah na arziqi ba, ina tasarrufi da su, kamar yadda na ga dama, kuma ba zan ce da ku, ni na san gaibu ba, sai abin da Allah ya tsinkayar da ni, na daga wahayi. Ba zan ce da ku, ni Mala’ika ne daga cikin Mala’iku ba, ni manzo ne daga Allah, bana bin komai sai abin da aka yi min wahayi da shi, ba na da’awar abin da ba nawa ba”. Ya kai wannan Manzo ka ce da su,: “Shin kafirin da basirarsa ta makance daga gaskiya, zai yi daidai da muminin da ya ga gaskita, kuma ya yi imani da ita?”. Ba kwa lura da ayoyin da suke kewaye da ku, da hankulanku – ya ku mushirikai.**

**51 Ya kai wannan Manzo ka tsoratar da waxanda suke jin tsoron a tara su a gaban Ubangijinsu ranar alqiyama da wannan Alqur’ani, ba su da wani majivincin lamari koma bayan Allah, da zai jawo musu amfani, ko wani mai ceto da zai yaye musu cuta. Wataqila su ji tsoron Allah ta hanyar kamanta umarninsa da nisantar abubuwan da ya hana. Waxannan su ne suke amfana da Alqur’ani.**

**52 Ya kai wannan Manzo ka da ka nisantar da talakawan musulmi daga majalisinka, waxanda suke cikin ibadar Allah a koyaushe, a farkon rana da qarshenta, suna masu tsarkake ibada ga Allah. Kada ka nisantar da su, don ka jawo hankulan manya-manyan mushirikai. Hisabin waxannan talakawan ba ya kanka da komai, kaxai hisabinsu yana wajen Ubangijinsu, suma hisabinka ba ya kansu da komai. Idan ka nisantar da su daga majalisinka, to zaka kasance cikin waxanda suka ketare iyakokin Allah.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Annabawa mutane ne, basu da abubuwan Allantaka a tare da su. Aikinsu shi ne isar da saqo, ba sa mallakar juya duniya, basu san gaibu ba, basa mallakar taskokin arziqi da makamantansu.**

**2 - Bayanin yadda mai da’awa zai damu da mabiyansa, musamman ma waxannan talakawan, waxanda ba sa neman komai sai gaskiya, wajibi a kansa ya kusantar da su, kada ya yarda da nisantar da su don neman yardar kafirai. 3 - Ayar ta nuna mahimmancin ibadun da ake yi a farkon rana da qarshenta.**

وَكَذَٰلِكَ فَتَنَّا بَعْضَهُم بِبَعْضٍ لِّيَقُولُوٓا۟ أَهَٰٓؤُلَآءِ مَنَّ ٱللَّهُ
عَلَيْهِم مِّنۢ بَيْنِنَآ ۗ أَلَيْسَ ٱللَّهُ بِأَعْلَمَ بِٱلشَّٰكِرِينَ ٥٣ وَإِذَا
جَآءَكَ ٱلَّذِينَ يُؤْمِنُونَ بِـَٔايَٰتِنَا فَقُلْ سَلَٰمٌ عَلَيْكُمْ ۖ كَتَبَ
رَبُّكُمْ عَلَىٰ نَفْسِهِ ٱلرَّحْمَةَ ۖ أَنَّهُۥ مَنْ عَمِلَ مِنكُمْ سُوٓءًۢا
بِجَهَٰلَةٍ ثُمَّ تَابَ مِنۢ بَعْدِهِۦ وَأَصْلَحَ فَأَنَّهُۥ غَفُورٌ رَّحِيمٌ ٥٤
وَكَذَٰلِكَ نُفَصِّلُ ٱلْءَايَٰتِ وَلِتَسْتَبِينَ سَبِيلُ ٱلْمُجْرِمِينَ
٥٥ قُلْ إِنِّى نُهِيتُ أَنْ أَعْبُدَ ٱلَّذِينَ تَدْعُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ ۚ قُل
لَّآ أَتَّبِعُ أَهْوَآءَكُمْ ۙ قَدْ ضَلَلْتُ إِذًا وَمَآ أَنَا۠ مِنَ ٱلْمُهْتَدِينَ
٥٦ قُلْ إِنِّى عَلَىٰ بَيِّنَةٍ مِّن رَّبِّى وَكَذَّبْتُم بِهِۦ ۚ مَا عِندِى مَا
تَسْتَعْجِلُونَ بِهِۦٓ ۚ إِنِ ٱلْحُكْمُ إِلَّا لِلَّهِ ۖ يَقُصُّ ٱلْحَقَّ ۖ وَهُوَ
خَيْرُ ٱلْفَٰصِلِينَ ٥٧ قُل لَّوْ أَنَّ عِندِى مَا تَسْتَعْجِلُونَ بِهِۦ لَقُضِىَ
الحزب ١٤ ٱلْأَمْرُ بَيْنِى وَبَيْنَكُمْ ۗ وَٱللَّهُ أَعْلَمُ بِٱلظَّٰلِمِينَ ٥٨ ۞ وَعِندَهُۥ
مَفَاتِحُ ٱلْغَيْبِ لَا يَعْلَمُهَآ إِلَّا هُوَ ۚ وَيَعْلَمُ مَا فِى ٱلْبَرِّ
وَٱلْبَحْرِ ۚ وَمَا تَسْقُطُ مِن وَرَقَةٍ إِلَّا يَعْلَمُهَا وَلَا حَبَّةٍ فِى ظُلُمَٰتِ
ٱلْأَرْضِ وَلَا رَطْبٍ وَلَا يَابِسٍ إِلَّا فِى كِتَٰبٍ مُّبِينٍ ٥٩



**(53) Haka nan muka jarrabi sashensu da sashe, muka sanya su mabambanta a wajen samun rabon duniya. Mun jarrabe su da haka, don mawadatan kafirai su cewa talakawan muminai: "Waxannan talakawan ne waxanda Allah ya yi wa falalar shiriya daga cikinmu?. Da imani alheri ne da ba zasu riga mu zuwa gare shi ba, mu masu riga mutane ne zuwa abu". Ashe Allah bai fi kowa sanin masu gode wa ni'imarsa ba, sai ya datar da su zuwa ga imani, kuma shi ne mafi sanin kafirai, sai ya tavar da su, ba zasu yi imani ba?!. Haka abun yake, Allah ya fi kowa saninsu.**

**(54) Ya kai wannan Manzo idan waxanda suka yi imani da ayoyinmu, kuma suka yi shaida a kan gaskiyar abin da ka zo da shi, suka zo wajenka, to ka mayar musu da sallama don girmama su, ka yi musu bushara da yalwar rahamar Allah. Haqiqa Allah ya wajabta wa kansa rahama, wajabta wa ta falala ba ta dole ba, duk wanda ya aikata savo cikin jahilci da wauta, sannan ya tuba daga baya, ya gyara aikinsa, to haqiqa Allah zai gafarta masa abin da ya aikata. Allah mai yawan gafara ne ga wanda ya tuba daga cikin bayinsa, mai jinqai ne.**

**(55) Kamar yadda muka bayyana maka abin da aka ambata, haka muke bayyana dalilanmu da hujjojinmu a kan mavarnata, don hanyar masu laifi da salonsu ya fito fili, don a nisance ta a kiyaye ta.**

**(56) Ka ce – ya kai wannan Manzo –: "Ni Allah ya hana ni bauta wa abin da kuke bauta wa koma bayan Allah". Ka ce – ya kai wannan Manzo –: "Ba zan bi abubuwan da zuciyoyinku suke son bi ba, wajen bauta wa wanin Allah. saboda idan na bi son zukatanku a cikin hakan, zan kasance vatacce daga hanyar gaskiya, ba zan gane ta ba, wannan shi ne sha'anin duk wanda ya bi son zuciya bada wata hujja daga wajen Allah ba".**

**(57) Ka cewa waxannan mushirikai – ya kai wannan Annabi – "Ni ina kan hujja bayyananniya daga Ubangijina, ba a kan son zuciya nake ba, ku kuma kun qaryata wannan hujja, amma ku sani abin da kuke gaggawar nema na azaba da ayoyin da suka savawa al'ada, basa hannuna, kaxai suna hannun Allah ne, kuma dukkan hukunci – har da abin da kuka nema – na Allah ne shi kaxai. Allah yana faxar gaskiya yana hukunci da ita. Kuma shi ne mafi alherin wanda yake bayyana gaskiya, ya tantance mai gaskiya da mavarnaci".**

**(58) Ka ce musu – ya kai wannan Manzo – Da abin da kuke gaggawar nema na azaba yana hannuna, da na saukar da shi a kanku, a wannan lokaci za a yanke lamarin da yake tsakanina da ku. Allah shi ne mafi sanin azzalumai, ya san zuwa wane lokaci zai jinkirta musu, kuma yaushe zai yi musu azaba.**

**(59) A wajen Allah shi kaxai taskokin gaibu suke, ba wanda ya san su, sai shi, ya san abin da yake kan tudu na halittu, na daga dabbobi da tsirrai da daskararrun abubuwa. Ya san abin da yake cikin kogi na daga dabbobi da tsirrai. Babu wani ganye da zai faxo a kowane wuri, ba wata qwaya voyayya a cikin qasa, ba za a samu wani xanye ba, ko busasshe, face sai ya kasance a cikin littafi bayyananne, shi ne lauhul Mahfuz.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Allah yana sanya bayi, sashensu ya zama jarraba ga sashe, darajojinsu su bambanta a wajen arziqi da kafirci da imani. Yalwata arziqi ko quntata shi bai da alaqa da kafirci ko imani.**

**2 - Yana daga cikin halayen mai wa'azi sakin fuska da yin sallama, da sakewa da farin ciki da abokansa.**

**3 - Ya wajaba a kan mai wa'azi ya nisanci son zuciya a cikin aqidarsa da salonsa da halayensa.**

**4 - Tabbatar da kaxaitakar Allah shi kaxai da sanin gaibu, bai da abokin tarayya, haka ma wajen yalwar ilimi, babu abin da yake kubce masa, ko yake vuya gare shi, daga cikin halittunsa, face wannan abun yana tabbace, a rubuce a wajensa, Allah (S.W.T) daki-daki, filla-filla.**

وَهُوَ ٱلَّذِي يَتَوَفَّىٰكُم بِٱلَّيۡلِ وَيَعۡلَمُ مَا جَرَحۡتُم بِٱلنَّهَارِ ثُمَّ
يَبۡعَثُكُمۡ فِيهِ لِيُقۡضَىٰٓ أَجَلٞ مُّسَمّٗىۖ ثُمَّ إِلَيۡهِ مَرۡجِعُكُمۡ ثُمَّ
يُنَبِّئُكُم بِمَا كُنتُمۡ تَعۡمَلُونَ ٦٠ وَهُوَ ٱلۡقَاهِرُ فَوۡقَ عِبَادِهِۦۖ
وَيُرۡسِلُ عَلَيۡكُمۡ حَفَظَةً حَتَّىٰٓ إِذَا جَآءَ أَحَدَكُمُ ٱلۡمَوۡتُ تَوَفَّتۡهُ
رُسُلُنَا وَهُمۡ لَا يُفَرِّطُونَ ٦١ ثُمَّ رُدُّوٓاْ إِلَى ٱللَّهِ مَوۡلَىٰهُمُ ٱلۡحَقِّۚ
أَلَا لَهُ ٱلۡحُكۡمُ وَهُوَ أَسۡرَعُ ٱلۡحَٰسِبِينَ ٦٢ قُلۡ مَن يُنَجِّيكُم مِّن
ظُلُمَٰتِ ٱلۡبَرِّ وَٱلۡبَحۡرِ تَدۡعُونَهُۥ تَضَرُّعٗا وَخُفۡيَةٗ لَّئِنۡ أَنجَىٰنَا مِنۡ
هَٰذِهِۦ لَنَكُونَنَّ مِنَ ٱلشَّٰكِرِينَ ٦٣ قُلِ ٱللَّهُ يُنَجِّيكُم مِّنۡهَا وَمِن كُلِّ كَرۡبٖ
ثُمَّ أَنتُمۡ تُشۡرِكُونَ ٦٤ قُلۡ هُوَ ٱلۡقَادِرُ عَلَىٰٓ أَن يَبۡعَثَ عَلَيۡكُمۡ عَذَابٗا مِّن
فَوۡقِكُمۡ أَوۡ مِن تَحۡتِ أَرۡجُلِكُمۡ أَوۡ يَلۡبِسَكُمۡ شِيَعٗا وَيُذِيقَ بَعۡضَكُم
بَأۡسَ بَعۡضٍۗ ٱنظُرۡ كَيۡفَ نُصَرِّفُ ٱلۡأٓيَٰتِ لَعَلَّهُمۡ يَفۡقَهُونَ ٦٥ وَكَذَّبَ
بِهِۦ قَوۡمُكَ وَهُوَ ٱلۡحَقُّۚ قُل لَّسۡتُ عَلَيۡكُم بِوَكِيلٖ ٦٦ لِّكُلِّ نَبَإٖ
مُّسۡتَقَرّٞۚ وَسَوۡفَ تَعۡلَمُونَ ٦٧ وَإِذَا رَأَيۡتَ ٱلَّذِينَ يَخُوضُونَ فِيٓ ءَايَٰتِنَا
فَأَعۡرِضۡ عَنۡهُمۡ حَتَّىٰ يَخُوضُواْ فِي حَدِيثٍ غَيۡرِهِۦۚ وَإِمَّا يُنسِيَنَّكَ
ٱلشَّيۡطَٰنُ فَلَا تَقۡعُدۡ بَعۡدَ ٱلذِّكۡرَىٰ مَعَ ٱلۡقَوۡمِ ٱلظَّٰلِمِينَ ٦٨



**(60) Allah Shi ne wanda yake karve rayukanku a wajen bacci, karva ta xan lokaci kaxan, kuma shi ne wanda ya san abin da kuke aikatawa da rana lokacin nishaxinku, sannan ya tashe ku da rana bayan karve rayukanku a cikin barci, don ku tashi don yin ayyukanku, har ajalin rayuwarku wanda aka qaddara muku a wajen Allah ya qare, sannan gare shi kaxai zaku koma bayan tashi a ranar alqiyama, sannan ya baku labarin abin da kuke aikatawa a rayuwarku ta duniya, ya saka muku a kansa.**
**(61) Allah ne mai rinjaye a kan bayinsa, masu qasqanta gare shi , shi ne maxaukaki a kansu ta kowane vangare, wanda dukkan komai ya sunkuya gare shi, yana saman bayinsa, kamar yadda ya dace da girmansa (S.W.T). Yana aiko muku – ya ku mutane – da Mala'iku masu girma, suna qirge ayyukanku, har idan ajalin xayanku ya qare Mala'ikan mutuwa da mataimakansa su karve ransa, ba sa gazawa wajen yin abin da aka umarce su da shi.**
**(62) Sannan aka mayar da duk wanda aka karvi rayukansu zuwa ga Allah, Mamallakinsu na gaskiya, don ya saka musu a kan ayyukansu. Allah wanda yake da hukunci zartatte a kansu, da hukunci na adalci. Shi ne mafi gaggawar qirge su da ayyukansu.**
**(63) Ya kai wannan Manzo ka cewa waxannan mushirikai: "Waye yake tseratar da ku, ya kuvutar da ku daga halaka, wadda kuke faxa wa cikinta, a cikin duhun tudu da kogi? Kuna kiransa shi kaxai, kuna masu qasqantar da kai, a fili da voye, (kuna cewa) idan ka kuvutar da mu ya Ubangijinmu, daga wannan halaka, zamu kasance cikin masu godiya, saboda ni'imarsa da ya yi mana, na rashin bauta wa waninsa. (64) Ya wannan Manzo ka ce da su: "Allah Shi ne wanda yake tseratar da ku daga wannan halaka, ya kuvutar da ku daga dukkan wata damuwa, sannan ku kuma bayan haka kuke haxa shi da wani a lokacin da kuke cikin yalwa da farin ciki, to wanne zalunci ne ya fi wannan da kuke yi?!". (65) Ka ce da su – Ya wannan Manzo –: "Allah mai iko ne a kan ya aiko muku da azaba, ta zo muku ta samanku, kamar duwatsu da tsawa da ruwan xufana, ko ta zo muku ta qasanku, kamar girgizar qasa, da kisfewa, ko kuma ya sava tsakanin zukatanku, kowa ya bi son zuciyarsa, wannan sashe ya yaqi wancan sashe". Ka lura – ya kai wannan Manzo – ta yaya muke cancanza musu dalilai da hujjoji, muke bayyana su, ko za su fahimta cewa abin da ka zo da shi gaskiya ne, abin da yake wajensu qarya ne. (66) Mutanenka sun qaryata da wannan Alqur'ani, alhali shi ne gaskiyar da babu shakka a cikinsa, kuma daga wajen Allah yake. Ka ce da su – ya wannan Manzo –: "Ba a xora min nauyin kula da ku ba. ni ba kowa ba ne face mai muku gargaxi gabanin zuwan azaba mai tsanani". (67) Kowane labari yana da matabbatarsa, da yake tabbata a cikinta, da qarshensa da yake tuqewa zuwa gare shi, daga cikin haka akwai qarshenku da makomarku, da sannu zaku san haka, a yayin da za a tashe ku ranar alqiyama. (68) Ya kai wannan Manzo idan ka ga waxannan mushirikai suna maganganu a kan ayoyinmu, da izgili, to ka nisance su, har sai sun shiga wani zancen da babu izgili ga ayoyinmu a cikinsa. Idan Shaixan ya mantar da kai, har ka zauna da su, sannan ka tuna, to ka bar majalisinsu, kada ka zauna da waxannan masu ketare iyaka.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:** **1 - Tabbatar da cewa barci mutuwa ne, kuma rayuka ana karvarsu a cikin barci, sannan a dawo da su yayin farkawa. 2 - Kafa dalili a kan cancantar Allah Maxaukakin Sarki da Allantaka ta hanyar hankalin da aka halicci mutum da shi. Kafirai suna yin imani da Allah, suna komawa hankalinsu yayin buqata, ko faxawa cikin halaka, sai su roqi Allah shi kaxai. 3 - Lazimta wa mushirikai abin da halayensu suka nuna, da tsayar da dalili a kan canzawar abin da aka halicce su a kai, saboda suna neman taimakon Allah shi kaxai yayin da suke cikin kogi da tsanani, suna shirka da Allah yayin da ya kuvutar da su, ya tseratar da su zuwa tudu. 4 - Rashin halaccin zama a majalisin mavarnata da wasannin banza, da halaccin barinsu da rashin dawowa gare su, sai dai idan sun bar abin da suke yi.**

وَمَا عَلَى ٱلَّذِينَ يَتَّقُونَ مِنْ حِسَابِهِم مِّن شَيْءٍ وَلَٰكِن
ذِكْرَىٰ لَعَلَّهُمْ يَتَّقُونَ ٦٩ وَذَرِ ٱلَّذِينَ ٱتَّخَذُوا۟ دِينَهُمْ
لَعِبًا وَلَهْوًا وَغَرَّتْهُمُ ٱلْحَيَوٰةُ ٱلدُّنْيَا ۚ وَذَكِّرْ بِهِۦٓ أَن
تُبْسَلَ نَفْسٌۢ بِمَا كَسَبَتْ لَيْسَ لَهَا مِن دُونِ ٱللَّهِ وَلِىٌّ
وَلَا شَفِيعٌ وَإِن تَعْدِلْ كُلَّ عَدْلٍ لَّا يُؤْخَذْ مِنْهَآ ۗ أُو۟لَٰٓئِكَ
ٱلَّذِينَ أُبْسِلُوا۟ بِمَا كَسَبُوا۟ ۖ لَهُمْ شَرَابٌ مِّنْ حَمِيمٍ
وَعَذَابٌ أَلِيمٌۢ بِمَا كَانُوا۟ يَكْفُرُونَ ٧٠ قُلْ أَنَدْعُوا۟ مِن دُونِ
ٱللَّهِ مَا لَا يَنفَعُنَا وَلَا يَضُرُّنَا وَنُرَدُّ عَلَىٰٓ أَعْقَابِنَا بَعْدَ إِذْ
هَدَىٰنَا ٱللَّهُ كَٱلَّذِى ٱسْتَهْوَتْهُ ٱلشَّيَٰطِينُ فِى ٱلْأَرْضِ
حَيْرَانَ لَهُۥٓ أَصْحَٰبٌ يَدْعُونَهُۥٓ إِلَى ٱلْهُدَى ٱئْتِنَا ۗ قُلْ إِنَّ
هُدَى ٱللَّهِ هُوَ ٱلْهُدَىٰ ۖ وَأُمِرْنَا لِنُسْلِمَ لِرَبِّ ٱلْعَٰلَمِينَ ٧١ وَأَنْ
أَقِيمُوا۟ ٱلصَّلَوٰةَ وَٱتَّقُوهُ ۚ وَهُوَ ٱلَّذِىٓ إِلَيْهِ تُحْشَرُونَ ٧٢ وَهُوَ
ٱلَّذِى خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضَ بِٱلْحَقِّ ۖ وَيَوْمَ يَقُولُ كُن
فَيَكُونُ ۚ قَوْلُهُ ٱلْحَقُّ ۚ وَلَهُ ٱلْمُلْكُ يَوْمَ يُنفَخُ فِى ٱلصُّورِ ۚ
عَٰلِمُ ٱلْغَيْبِ وَٱلشَّهَٰدَةِ ۚ وَهُوَ ٱلْحَكِيمُ ٱلْخَبِيرُ ٧٣



**69 Babu hisabin waxannan azzalumai a kan waxanda suke jin tsoron Allah, ta hanyar kamanta umarninsa da nisantar abubuwan da ya hana, kawai abin da yake kansu shi ne su hana su munanan abin da suke aikatawa, ko sa ji tsoron Allah, su kamanta umarninsa, su nisanci abin da ya hana.**

**70 Ya kai wannan Manzo ka kyale waxannan mushirikai, waxanda suka mayar da addininsu wasa da wargi, suna masa izgili, suna wasa da shi, rayuwar duniya ta ruxe su, da xan abin da yake cikinta na jin daxi mai gushewa. Ka yi wa mutane wa'azi da Alqur'ani – ya kai wannan Annabi – don kada wata rai ta kai zuwa ga halaka, saboda abin da ta aikata na munanan ayyuka, bata da wani mataimaki koma bayan Allah, da zai taimake ta, ko wani xan-tsakani da zai kare ta daga azabar Allah ranar alqiyama. Idan da za a fanshe ta daga azabar Allah da kowace irin fansa, ba za a karva daga gare ta ba. Waxannan da suka sallama kansu ga halaka, saboda da abin da suka aikata na munanan ayyuka, suna da abin sha mai tsananin zafi, da azaba mai ciwo saboda kafircinsu.**

**71 Ya kai wannan manzo ka cewa waxannan mushirikai: Kuna bauta wa wanin Allah daga gumaka, waxanda ba sa mallakar amfani, ballantana su amfane mu, ko cuta bare su cuce mu, har mu bar imani bayan Allah ya datar da mu zuwa gare shi, mu zama kamar waxanda Shaixanu suka vatar da shi, suka bar shi a ruxe, baya gane hanya. Yana da abokai a kan tafarki madaidaici, suna kiran shi zuwa ga gaskiya, shi kuma yana qin amsa musu zuwa ga abin da suke kiransa zuwa gare shi. Ka ce da su – ya kai wannan Manzo –: "Haqiqa shiriyar Allah ita ce shiriyar gaskiya. Kuma Allah ya umarce mu mu jayu zuwa gare shi, mu lazimci kaxaita Allah da bauta shi kaxai, don shi ne Ubangijin talikai.**

**72 Tabbas ya umarce mu da tsaida sallah, a kan kama cikakkiya, ya umarce mu da tsoron Allah, ta hanyar kamanta umarninsa da nisantar abubuwan da ya hana. Shi kaxai ne wanda ake tara bayi zuwa gare shi, ranar alqiyama, don ya saka musu a kan ayyukansu.**

**73 Allah mai girma da buwaya shi ne wanda ya halicci sammai da qassai da gaskiya, ranar da Allah zai cewa abu: "Kasance", sai ya kasance, a yayin da zai ce a ranar alqiyama: "ku tashi, sai su tashi". Maganarsa gaskiya ce, wadda zata faru babu makawa, Shi kaxai yake mulki ranar alqiyama, ranar da Mala'ika Israfilu zai yi busa a qaho busa ta biyu. Masanin abin da yake voye, Masanin abin da ake gani. Shi ne mai hikima a cikin halittarsa, da tsarinsa, Masanin da babu abin da yake vuya gare shi, voyayyun abubuwa a wajensa kamar bayyanannu ne.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Mai kira zuwa ga addinin Allah, ba za a tambaye shi a kan kowa ba, kawai za a tambaye shi ne a kan isar da saqo da tunatarwa.**

**2 - Wa'azi yana daga cikin mafi girman hanyoyin faxakar da gafalallu da masu girman kai.**

**3 - Yana daga cikin dalilan tauhidi: Wanda baya mallakar amfani ko cuta ko juya al'amura, to a hankalce bai cancanta ya zama Allah abin bautawa ba.**

الحزب ١٤

۞ وَإِذْ قَالَ إِبْرَٰهِيمُ لِأَبِيهِ ءَازَرَ أَتَتَّخِذُ أَصْنَامًا ءَالِهَةً إِنِّيٓ
أَرَىٰكَ وَقَوْمَكَ فِي ضَلَٰلٖ مُّبِينٖ ﴿٧٤﴾ وَكَذَٰلِكَ نُرِيٓ إِبْرَٰهِيمَ
مَلَكُوتَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ وَلِيَكُونَ مِنَ ٱلْمُوقِنِينَ
﴿٧٥﴾ فَلَمَّا جَنَّ عَلَيْهِ ٱلَّيْلُ رَءَا كَوْكَبٗاۖ قَالَ هَٰذَا رَبِّيۖ فَلَمَّآ أَفَلَ
قَالَ لَآ أُحِبُّ ٱلْأٓفِلِينَ ﴿٧٦﴾ فَلَمَّا رَءَا ٱلْقَمَرَ بَازِغٗا قَالَ هَٰذَا
رَبِّيۖ فَلَمَّآ أَفَلَ قَالَ لَئِن لَّمْ يَهْدِنِي رَبِّي لَأَكُونَنَّ مِنَ ٱلْقَوْمِ
ٱلضَّآلِّينَ ﴿٧٧﴾ فَلَمَّا رَءَا ٱلشَّمْسَ بَازِغَةٗ قَالَ هَٰذَا رَبِّي هَٰذَآ
أَكْبَرُۖ فَلَمَّآ أَفَلَتْ قَالَ يَٰقَوْمِ إِنِّي بَرِيٓءٞ مِّمَّا تُشْرِكُونَ
﴿٧٨﴾ إِنِّي وَجَّهْتُ وَجْهِيَ لِلَّذِي فَطَرَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضَ
حَنِيفٗاۖ وَمَآ أَنَا۠ مِنَ ٱلْمُشْرِكِينَ ﴿٧٩﴾ وَحَآجَّهُۥ قَوْمُهُۥۚ قَالَ
أَتُحَٰٓجُّوٓنِّي فِي ٱللَّهِ وَقَدْ هَدَىٰنِۚ وَلَآ أَخَافُ مَا تُشْرِكُونَ بِهِۦٓ
إِلَّآ أَن يَشَآءَ رَبِّي شَيْـٔٗاۚ وَسِعَ رَبِّي كُلَّ شَيْءٍ عِلْمًاۚ أَفَلَا
تَتَذَكَّرُونَ ﴿٨٠﴾ وَكَيْفَ أَخَافُ مَآ أَشْرَكْتُمْ وَلَا تَخَافُونَ
أَنَّكُمْ أَشْرَكْتُم بِٱللَّهِ مَا لَمْ يُنَزِّلْ بِهِۦ عَلَيْكُمْ سُلْطَٰنٗاۚ
فَأَيُّ ٱلْفَرِيقَيْنِ أَحَقُّ بِٱلْأَمْنِۖ إِن كُنتُمْ تَعْلَمُونَ ﴿٨١﴾



**(74) Ka tuna – ya kai wannan manzo – yayin da Annabi Ibrahim (A.S) ya ce wa babansa Aazara, wanda yake mushiriki ne, ya ce masa: "Ya babana, yanzu zaka sanya gumaka alloli, kana bauta musu koma bayan Allah?! Haqiqa ina ganinka da mutanenka waxanda suke bauta wa gumaka a cikin vata mai girma, da ruxewa daga barin hanya, saboda bauta wa wanin Allah da kuke yi, Alhali Allah (S.W.T) shi ne abin bauta wa da gaskiya. Waninsa kuwa abin bauta ne na qarya.**

**(75) Kamar yadda muka nuna masa vatan babansa da mutanensa, haka muka nuna masa mulkin sammai da qassai masu girma, saboda ya kafa hujja da wannan mulki mai faxi a kan kaxaitakar Allah da cancantar shi da bauta, kuma don ya zama cikin masu yaqini a kan Allah xaya ne, shi kaxai, ba shi da abokin tarayya, kuma shi mai iko ne a kan dukkan komai.**

**(76) Yayin da dare ya yi duhu, sai Annabi Ibrahim ya ga tauraro, sai ya ce,: "Wannan shi ne Ubangijina". Amma yayin da tauraron ya vace, sai ya ce,: " Kai! bana son abin da yake vacewa, saboda Allan gaskiya yana nan, ba ya vacewa".**

**(77) Yayin da ya ga wata, ya vullo, sai ya ce,: "Wannan ne Ubangijina". Amma Yayin da ya vace, sai ya ce, Idan Allah bai datar da ni ga kaxaita shi, da bauta masa shi kaxai ba, to zan kasance cikin mutanen da suka yi nisa da addinin gaskiya".**

**(78) Yayin da ya ga rana ta fito, sai ya ce,: "Wannan da ta fito ita ce Ubangijina, kuma wannan ta fi tauraro da wata girma". Amma yayin da ta faxi, sai ya ce,: "Ya Mutane na, haqiqa ni na barranta daga abin da kuke haxa Allah da shi wajen bauta".**

**Yayin da ya barranta daga abin da suke bauta wa koma bayan Allah, sai ya zama kamar sun tambaye shi, to me kake bauta wa kenan? Sai ya basu amsa ya ce,:**

**(79) "Haqiqa ni na tsarkake addinina ga wanda ya halicci sammai da qassai, ba tare da ya gani a wurin wani ba, na karkata daga barin shirka zuwa ga kaxaita Allah (wato tauhid) tsakakakke, kuma bana cikin mushirikai, masu haxa Allah da wani, suna bauta masa tare da shi".**

**(80) Mutanensa mushirikai sun yi jayayya da shi a kan kaxaita Allah (Tauhid) , suka tsoratar da shi da gumakansu, sai ya ce da su: "Yanzu kuna jayayya da ni a kan kaxaita Allah da bauta, alhali Ubangijina ya datar da ni zuwa gare shi, to bana jin tsoron gumakanku, domin ba sa mallakar cutarwa, ballantana su cuce ni, haka ma basa mallakar amfani, ballantana su amfane ni, sai dai da abin da Allah ya ga dama. Duk abin da Allah ya ga dama shi yake kasancewa. Saboda Allah ya san komai, babu abin da yake vuya a gare shi, a cikin qasa da sama. Ya ku mutanena baza ku wa'azantu ba a kan abin da kuke kai na kafirci da haxa Allah da wani (Wato Shirka) , ku yi imani da Allah shi kaxai ba?!".**

**(81) Ta yaya zan ji tsoron abin da kuke bauta wa koma bayan Allah na gumaka, alhali ku ba zaku ji tsoron haxa Allah da abin da ya halitta, da kuke yi ba, ba tare da wata hujja a kan haka ba?!. To waxanne jama'a ne cikinmu – wato jama'ar masu kaxaita Allah da jama'ar masu haxa Allah da wani (wato mushirikai) - suka fi cancanta su samu aminci da tsira?!. In dai har kun san waxanda suka fi cancanta xin, to ku bi su. Waxanda suka fi cancanta, ko shakka babu, su ne jama'ar da suke kaxaita Allah wato muminai.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Kafa hujja da ayyukan Allah (Wato Rububiyyah) ta hanyar duba zuwa ga halittunsa, wani salo ne na Alqur'ani.**

**2 - Dalilai na hankali bayyanannu suna kai wa zuwa ga kaxaita Allah da ayyukansa.**

ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَلَمۡ يَلۡبِسُوٓاْ إِيمَٰنَهُم بِظُلۡمٍ أُوْلَٰٓئِكَ لَهُمُ ٱلۡأَمۡنُ
وَهُم مُّهۡتَدُونَ ٨٢ وَتِلۡكَ حُجَّتُنَآ ءَاتَيۡنَٰهَآ إِبۡرَٰهِيمَ عَلَىٰ
قَوۡمِهِۦۚ نَرۡفَعُ دَرَجَٰتٖ مَّن نَّشَآءُۗ إِنَّ رَبَّكَ حَكِيمٌ عَلِيمٞ ٨٣
وَوَهَبۡنَا لَهُۥٓ إِسۡحَٰقَ وَيَعۡقُوبَۚ كُلًّا هَدَيۡنَاۚ وَنُوحًا هَدَيۡنَا
مِن قَبۡلُۖ وَمِن ذُرِّيَّتِهِۦ دَاوُۥدَ وَسُلَيۡمَٰنَ وَأَيُّوبَ وَيُوسُفَ
وَمُوسَىٰ وَهَٰرُونَۚ وَكَذَٰلِكَ نَجۡزِي ٱلۡمُحۡسِنِينَ ٨٤
وَزَكَرِيَّا وَيَحۡيَىٰ وَعِيسَىٰ وَإِلۡيَاسَۖ كُلّٞ مِّنَ ٱلصَّٰلِحِينَ
٨٥ وَإِسۡمَٰعِيلَ وَٱلۡيَسَعَ وَيُونُسَ وَلُوطٗاۚ وَكُلّٗا فَضَّلۡنَا عَلَى
ٱلۡعَٰلَمِينَ ٨٦ وَمِنۡ ءَابَآئِهِمۡ وَذُرِّيَّٰتِهِمۡ وَإِخۡوَٰنِهِمۡۖ وَٱجۡتَبَيۡنَٰهُمۡ
وَهَدَيۡنَٰهُمۡ إِلَىٰ صِرَٰطٖ مُّسۡتَقِيمٖ ٨٧ ذَٰلِكَ هُدَى ٱللَّهِ يَهۡدِي
بِهِۦ مَن يَشَآءُ مِنۡ عِبَادِهِۦۚ وَلَوۡ أَشۡرَكُواْ لَحَبِطَ عَنۡهُم مَّا كَانُواْ
يَعۡمَلُونَ ٨٨ أُوْلَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ ءَاتَيۡنَٰهُمُ ٱلۡكِتَٰبَ وَٱلۡحُكۡمَ
وَٱلنُّبُوَّةَۚ فَإِن يَكۡفُرۡ بِهَا هَٰٓؤُلَآءِ فَقَدۡ وَكَّلۡنَا بِهَا قَوۡمٗا لَّيۡسُواْ
بِهَا بِكَٰفِرِينَ ٨٩ أُوْلَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ هَدَى ٱللَّهُۖ فَبِهُدَىٰهُمُ ٱقۡتَدِهۡۗ
قُل لَّآ أَسۡـَٔلُكُمۡ عَلَيۡهِ أَجۡرًاۖ إِنۡ هُوَ إِلَّا ذِكۡرَىٰ لِلۡعَٰلَمِينَ ٩٠



**(82) Waxanda suka yi imani da Allah, suka bi abin da ya shar'anta, kuma ba su haxa imaninsu da shirka ba, to suna da cikakken aminci da tsira, su kaxai banda waninsu, kuma su ne waxanda aka datar, wato Ubangijinsu ya datar da su zuwa hanyar shiriya.**

**(83) Waccan hujjar. Ita ce faxin Allah (Waxanne jama'ane suka fi cancanta da aminci…) wadda Annabi Ibrahim ya yi galaba da ita a kan mutanensa, har suka kasa ba shi hujja, ita ce hujjarmu da muka datar da shi da ita, saboda ya kafawa mutanensa hujja da ita, mu muka ba shi ita. Muna xaga darajar waxanda muka ga dama daga cikin bayinmu a duniya da lahira. Haqiqa Ubangijinka – ya kai wannan Manzo – mai hikima ne a cikin halittarsa da tsarinsa, kuma masanin bayinsa ne.**

**(84) Mun arzurta Annabi Ibrahim da xansa Annabi Ishaq da jikansa Annabi Yaqub. Dukkaninsu mun datar da su ga hanya miqaqqiya. Mun datar da Annabi Nuhu a gabaninsu. Haka nan mun datar daga cikin zurriyarsa, Annabi Dawud da xansa Sulaiman, da Ayyuba, da Yusufu, da Musa da xan uwansa Haruna, mun datar da su zuwa ga hanya madaidaiciya. Irin wannan sakamakon da muka saka wa Annabawa da shi, saboda kyautatawarsu, haka muke sakawa masu kyautatawa a kan kyautatawarsu.**

**(85) Haka nan mun datar da Annabi Zakariyya da Yahya da Isa xan Maryam da Ilyas – Amincin Allah ya tabbata a gare su - . Dukkanin waxannan Annabawa ne salihai, waxanda Allah ya zave su, suka zama manzanni.**

**(86) Haka nan mun datar da Annabi Isma'il da Al-yasa'u da Yunus da Lux – Amincin Allah ya tabbata a gare su -. Dukkanin waxannan Annabawan, shugabansu Annabi Muhammad (S.A.W) mun fifita su a kan talikai.**

**(87) Mun datar da wasu daga cikin iyayensu da wasu daga cikin 'ya'yansu, da wasu daga cikin 'yan uwansu, da waxanda muka ga dama mu datar da su, mun zave su, mun datar da su ga bin hanya madaidaiciya, wadda ita ce hanyar kaxaita Allah (Tauhid) da biyayya gare shi.**

**(88) Wannan dacen da suka samu, shi ne dacen Allah da yake ba wanda ya ga dama daga cikin bayinsa, kuma da za su haxa Allah da wani (wato shirka) da ayyukansu sun vace, saboda shirka tana lalata ayyuka na qwarai.**

**(89) Waxancan Annabawa da aka ambata, mun ba su littattafai, mun ba su hikima, mun basu annabta, idan mutanenka sun kafirce wa waxannan abubuwan da muka ba su, to mun shirya musu wasu mutane waxanda ba za su kafirce musu ba, masu imani ne da su, masu riqo da su ne. Su ne Almuhajiruun (Wato Sahabban da suka yi hijira daga Makka zuwa Madinah) da Al-ansar (Wato Mutanen Madinah) da waxanda suka bi su da kyautatawa zuwa ranar sakamako.**

**(90) Waxancan annabawa, da waxanda aka ambata daga iyayensu da 'ya'yansu da 'yan uwansu, sune shiryayyu na haqiqa, ka bi su, ka yi koyi da su. Ka cewa mutanenka – Ya kai wannan Manzo – "Ba na neman wani lada a wurinku a kan isar muku da wannan Alqur'ani. Alqur'ani wa'azi ne ga talikai, mutane da aljannu, don su shiriya da shi zuwa ga hanya madaidaiciya, kuma ingantacciya".**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - Yana daga cikin falalar kaxaita Allah da bauta (Wato Tauhid) yana zama dalilin lamunce wa bawa samun aminci. Musamman ma a lahira yayin da mutane suke firgita. 2 - Ayoyi suna tabbatar da dukkan waxanda suka gabata daga Annabawa, sun isar da saqonsu ne a bisa datarwar Allah, ba wai da wayonsu ko ikon su ba ne. 3 - Annabawa gaba daya sun yi tarayya wajen kira zuwa ga kaxaita Allah da bauta (wato tauhid) duk da savanin shari'o'insu a wajen ibada.**
**4 - Koyi da Annabawa tafarki ne mai kyau, musamman ma a tushen addini (Wato tauhidi).**

وَمَا قَدَرُواْ ٱللَّهَ حَقَّ قَدۡرِهِۦٓ إِذۡ قَالُواْ مَآ أَنزَلَ ٱللَّهُ عَلَىٰ بَشَرٖ مِّن شَيۡءٖۗ
قُلۡ مَنۡ أَنزَلَ ٱلۡكِتَٰبَ ٱلَّذِي جَآءَ بِهِۦ مُوسَىٰ نُورٗا وَهُدٗى
لِّلنَّاسِۖ تَجۡعَلُونَهُۥ قَرَاطِيسَ تُبۡدُونَهَا وَتُخۡفُونَ كَثِيرٗاۖ وَعُلِّمۡتُم
مَّا لَمۡ تَعۡلَمُوٓاْ أَنتُمۡ وَلَآ ءَابَآؤُكُمۡۖ قُلِ ٱللَّهُۖ ثُمَّ ذَرۡهُمۡ فِي خَوۡضِهِمۡ
يَلۡعَبُونَ ٩١ وَهَٰذَا كِتَٰبٌ أَنزَلۡنَٰهُ مُبَارَكٞ مُّصَدِّقُ ٱلَّذِي بَيۡنَ
يَدَيۡهِ وَلِتُنذِرَ أُمَّ ٱلۡقُرَىٰ وَمَنۡ حَوۡلَهَاۚ وَٱلَّذِينَ يُؤۡمِنُونَ بِٱلۡأٓخِرَةِ
يُؤۡمِنُونَ بِهِۦۖ وَهُمۡ عَلَىٰ صَلَاتِهِمۡ يُحَافِظُونَ ٩٢ وَمَنۡ أَظۡلَمُ مِمَّنِ
ٱفۡتَرَىٰ عَلَى ٱللَّهِ كَذِبًا أَوۡ قَالَ أُوحِيَ إِلَيَّ وَلَمۡ يُوحَ إِلَيۡهِ شَيۡءٞ
وَمَن قَالَ سَأُنزِلُ مِثۡلَ مَآ أَنزَلَ ٱللَّهُۗ وَلَوۡ تَرَىٰٓ إِذِ ٱلظَّٰلِمُونَ فِي
غَمَرَٰتِ ٱلۡمَوۡتِ وَٱلۡمَلَٰٓئِكَةُ بَاسِطُوٓاْ أَيۡدِيهِمۡ أَخۡرِجُوٓاْ أَنفُسَكُمُۖ
ٱلۡيَوۡمَ تُجۡزَوۡنَ عَذَابَ ٱلۡهُونِ بِمَا كُنتُمۡ تَقُولُونَ عَلَى ٱللَّهِ غَيۡرَ
ٱلۡحَقِّ وَكُنتُمۡ عَنۡ ءَايَٰتِهِۦ تَسۡتَكۡبِرُونَ ٩٣ وَلَقَدۡ جِئۡتُمُونَا
فُرَٰدَىٰ كَمَا خَلَقۡنَٰكُمۡ أَوَّلَ مَرَّةٖ وَتَرَكۡتُم مَّا خَوَّلۡنَٰكُمۡ وَرَآءَ
ظُهُورِكُمۡۖ وَمَا نَرَىٰ مَعَكُمۡ شُفَعَآءَكُمُ ٱلَّذِينَ زَعَمۡتُمۡ أَنَّهُمۡ فِيكُمۡ
شُرَكَٰٓؤُاْۚ لَقَد تَّقَطَّعَ بَيۡنَكُمۡ وَضَلَّ عَنكُم مَّا كُنتُمۡ تَزۡعُمُونَ ٩٤



**(91) Mushirikai ba su girmama Allah haqiqanin girmamawa ba, yayin da suka cewa Annabin Allah Muhammad (S.A.W): "Ba wani mutum da Allah ya saukar wa da komai na daga wahayi". Ka ce da su – Ya kai wannan Manzo -: 'Waye ya saukar da Attaura ga Annabi Musa, tana mai haske da shiriya ga mutanensa?". Yahudawa sun mayar da Attaura a cikin qananan littattafai, suna bayyana abin da ya dace da son zuciyarsu, suna voye abin da ya savawa son zuciyarsu, kamar siffar Annabi Muhammad (S.A.W). Ya ku larabawa an sanar da ku, ku da magabatanku abin da baku sani ba daga cikin Alqur'ani,. Don haka ka ce da su – Ya kai wannan Manzo – Allah ne ya saukar da Attaura". Sannan ka bar su cikin vatansu da wautarsu har yaqini ya zo musu.**

**(92) Wannan Alqur'ani littafi ne da muka saukar maka – ya kai wannan Annabi- litttafi ne mai albarka, mai gasgata abin da ya gabace shi na littafan da suka sauka daga sama, kuma don ka gargaxi mutanen Makkah da sauran mutane da shi, gabas da yamma, har su shiriya. Waxanda suka yi imani da rayuwar lahira, suna yin imani da wannan Alqur'ani, suna yin aiki da abin da yake cikinsa, suna kiyaye sallarsu, ta hanyar tsaida rukunanta da farillanta da mustahabbanta, a kan lokutanta da aka iyakance mata a shari'a.**

**(93) Ba wanda ya fi girman zalunci irin wanda ya qirqiri qarya ga Allah, ya ce,: "Allah bai saukar wa da wani mutum komai ba", ko kuma ya yi qarya ya ce,: "Allah ya yi masa wahayi", alhali Allah bai yi masa wahayin komai ba, ko ya ce, "Ni ma zan saukar da irin abin da Allah ya saukar na Alqur'ani". Da zaka ga lokacin da mayen mutuwa yake samun waxannan azzalumai, Mala'iku sun shimfixa hannayensu a kansu, suna azabtar da su da dukansu, suna musu tsawa suna cewa, ku fito da rayukanku, mu karve su. Kuma a yau ne ake saka muku da azabar da zata wulaqantar da ku, ta qasqantar da ku, saboda abin da kuke faxa dangane da Allah na qarya, da da'awar Annabta, da wahayi, da saukar da abin da Allah bai saukar ba, kuma saboda girman kanku ga imani da ayoyinsa. Da zaka ga hakan, da ka ga al'amari mai ban tsoro.**

**(94) Ranar tsahin alqiyama za a ce da su: "Haqiqa yau kun zo mana ku kaxai, ba dukiya, ba mulki, kamar yadda muka samar da ku a farkon lamari, babu takalmi, tsirara, babu kaciya, kun bar abin da muka baku a bayanku a duniya, a kan dole. A yau bamu ga wasu alloli waxanda kuka riya cewa su ne tsani tsakaninku da Allah a tare da ku ba. Kuka riya cewa su abokan tarayya ne da Allah wajen bauta. Zumunci ya yanke a tsakaninku, abin da kuke riyawa na su masu ceto, abokan tarayyar Allah, duk ya vace muku".**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Karantarwa:

**1 - Saukar da littattafai ga Annabawa, sunnar Allah ce a cikin Manzanni. Annabi (S.A.W) xaya ne daga cikinsu.**

**2 - Wanda ya fi dukkan mutane qarya shi ne wanda yake wa Allah qarya, ya dangana masa wani abu, ko ya kore masa, ya tabbatar da wani haqqi ga Allah wanda babu wani dalili ingantacce a kai.**

**3 - Kowa za a tashe shi ranar alqiyama shi kaxai, ba wani muqami ko laqabi da za a kira shi da shi, kuma yana talaka, sannan shi kaxai za a yi wa hisabi.**

ثلاثة أرباع الحزب ١٤

۞ إِنَّ ٱللَّهَ فَالِقُ ٱلۡحَبِّ وَٱلنَّوَىٰۖ يُخۡرِجُ ٱلۡحَيَّ مِنَ ٱلۡمَيِّتِ وَمُخۡرِجُ
ٱلۡمَيِّتِ مِنَ ٱلۡحَيِّۚ ذَٰلِكُمُ ٱللَّهُۖ فَأَنَّىٰ تُؤۡفَكُونَ ٩٥ فَالِقُ ٱلۡإِصۡبَاحِ
وَجَعَلَ ٱلَّيۡلَ سَكَنٗا وَٱلشَّمۡسَ وَٱلۡقَمَرَ حُسۡبَانٗاۚ ذَٰلِكَ تَقۡدِيرُ
ٱلۡعَزِيزِ ٱلۡعَلِيمِ ٩٦ وَهُوَ ٱلَّذِي جَعَلَ لَكُمُ ٱلنُّجُومَ لِتَهۡتَدُواْ
بِهَا فِي ظُلُمَٰتِ ٱلۡبَرِّ وَٱلۡبَحۡرِۗ قَدۡ فَصَّلۡنَا ٱلۡأٓيَٰتِ لِقَوۡمٖ يَعۡلَمُونَ
٩٧ وَهُوَ ٱلَّذِيٓ أَنشَأَكُم مِّن نَّفۡسٖ وَٰحِدَةٖ فَمُسۡتَقَرّٞ وَمُسۡتَوۡدَعٞۗ
قَدۡ فَصَّلۡنَا ٱلۡأٓيَٰتِ لِقَوۡمٖ يَفۡقَهُونَ ٩٨ وَهُوَ ٱلَّذِيٓ أَنزَلَ مِنَ
ٱلسَّمَآءِ مَآءٗ فَأَخۡرَجۡنَا بِهِۦ نَبَاتَ كُلِّ شَيۡءٖ فَأَخۡرَجۡنَا مِنۡهُ
خَضِرٗا نُّخۡرِجُ مِنۡهُ حَبّٗا مُّتَرَاكِبٗا وَمِنَ ٱلنَّخۡلِ مِن طَلۡعِهَا قِنۡوَانٞ
دَانِيَةٞ وَجَنَّٰتٖ مِّنۡ أَعۡنَابٖ وَٱلزَّيۡتُونَ وَٱلرُّمَّانَ مُشۡتَبِهٗا وَغَيۡرَ
مُتَشَٰبِهٍۗ ٱنظُرُوٓاْ إِلَىٰ ثَمَرِهِۦٓ إِذَآ أَثۡمَرَ وَيَنۡعِهِۦٓۚ إِنَّ فِي ذَٰلِكُمۡ
لَأٓيَٰتٖ لِّقَوۡمٖ يُؤۡمِنُونَ ٩٩ وَجَعَلُواْ لِلَّهِ شُرَكَآءَ ٱلۡجِنَّ وَخَلَقَهُمۡۖ
وَخَرَقُواْ لَهُۥ بَنِينَ وَبَنَٰتِۭ بِغَيۡرِ عِلۡمٖۚ سُبۡحَٰنَهُۥ وَتَعَٰلَىٰ عَمَّا يَصِفُونَ
١٠٠ بَدِيعُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۖ أَنَّىٰ يَكُونُ لَهُۥ وَلَدٞ وَلَمۡ تَكُن لَّهُۥ
صَٰحِبَةٞۖ وَخَلَقَ كُلَّ شَيۡءٖۖ وَهُوَ بِكُلِّ شَيۡءٍ عَلِيمٞ ١٠١



**95 Allah ne kaxai yake tsaga qwaya, shuka ta fito daga cikinta, Ya tsaga qwallo dabino ya fito daga cikinsa. Yana fitar da rayayye daga matacce, saboda yana fitar da mutum da sauran dabbobi daga xigon maniyyi. Kuma yana fitar da matacce daga rayayye, don yana fitar da xigon maniyyi daga mutum, ya fitar da qwai daga Kaza. Wanda yake wannan shi ne Allah, wanda ya halicce ku, to ta yaya ake karkatar da ku – yaku mushirikai – daga gaskiyar da kuke ganinta na kyawawan abin da Allah ya aikata?!.**

**96 (Allah) shi ne wanda yake tsago hasken safiya daga duhun dare. Kuma shi ne wanda ya sanya dare ya zama nutsuwa ga mutane, suna nutsuwa a cikinsa, da barin kai-kawo daga neman abinci, saboda su huta daga gajiyar neman abincin da suka yi da rana. Allah shi ne wanda ya sanya rana da wata suna gudana a kan lissafin da ya qaddara musu. Wannan abin da aka ambata na kyakkyawan tsari, qaddarawar Allah ne Mabuwayi, wanda babu wanda yake rinjayarsa. Masanin halittarsa da abin da ya dace da su.**

**97 Ya ku 'yayan Adam (Allah) shi ne wanda ya halitta muku taurari a cikin sama, saboda ku gane hanya da su a tafiye-tafiyenku, yayin da hanyoyi suka rikice muku, a tudu da kogi. Mun bayyana dalilai da hujjoji masu nuna ikonmu, ga mutanen da suke lura da dalilai da hujjoji, kuma suke amfana da su.**

**98 Shi ne (Allah) wanda ya halicce ku daga rai xaya, ita ce ran babanku Annabi Adam. Haqiqa ya fara halittarku da halittar babanku daga tavo, sannan ya halicceku daga gare shi. Ya halitta muku inda zaku zauna a ciki, kamar mahaifar iyayenku, da inda za a ajiye ku, kamar cikin tsatson iyayenku maza. Haqiqa mun bayyana ayoyi ga mutanen da suke fahimtar zancen Allah.**

**99 Shi ne (Allah) wanda ya saukar da ruwa daga sama, sannan muka fitar da dukkan wata kala na 'ya'yan itace da wannan ruwa. Muka fitar da tsirrai, shuka, da koriyar bishiya. Muna fitar da qwaya wata kan wata kamar yadda suke a zargarniya da wannan ruwan. Muna fitar zarbar dabino daga hudar dabino, wanda yake zaune da wanda yake tsaye suna iya samunta. Mun fitar da gonaki na inabi. Mun fitar da Zaitun da Rumman masu ganyaye iri xaya, amma xanxano daban-daban. Ya ku mutane, Ku kalli 'ya'yan itacensa a farkon lokacin da ya fito, da lokacin da ya nuna. Ya ku mutane a cikin waxannan abubuwa akwai dalilai bayyanannu a kan ikon Allah ga mutanen da suka yi imani da Allah. Muminai su ne suke amfanuwa da waxannan dalilai da hujjoji.**

**100 Mushirikai sun mayar da aljannu abokan tarayyar Allah a wajen ibada, yayin da suka qudurce aljannu suna amfanar wa, suna cutarwa. Allah ya samar da su, ba wanda ya halicce su sai shi, don haka shi ya cancanta a bauta masa. Haka nan sun qirqirawa Allah 'ya'ya, kamar yadda Yahudawa suka yi a kan Uzairu, Nasara suka yi ga Annabi Isa. Suka sa wa Allah 'ya'ya mata kamar yadda mushirikai suka yi a kan Mala'iku. Allah ya tsarkaka daga abin da mavarnata suke siffata shi da shi.**

**101 Allah Shi ne mahallicin sammai da qassai, ba tare da ganin samfurinsu a wurin wasu ba. Ta yaya Allah zai zama yana da xa, alhali bai da mata?. Shi ne wanda ya halicci dukkan komai, kuma shi ga dukkan komai masani ne, babu abin da yake vuya gare shi.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Kafa hujja da halitta da arzurtawa (Kamar halittar tsirrai da yadda suke girma, da canzawarsu da girmansu da saukar da ruwa) da kafa hujja da dalilin motsi (kamar motsin falakai da tafiyarsu a bisa tsari) dukkan waxannan hujjoji guda biyu, ana ganinsu, kuma suna nuna kaxaitakar Allah da ayyukansa da cancantarsa da bauta.**

**2 - Bayanin vata da wawancin hankalin mushirikai a wajen bautar su ga Aljannu.**

ذَٰلِكُمُ ٱللَّهُ رَبُّكُمۡۖ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَۖ خَٰلِقُ كُلِّ شَيۡءٖ فَٱعۡبُدُوهُۚ
وَهُوَ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ وَكِيلٞ ١٠٢ لَّا تُدۡرِكُهُ ٱلۡأَبۡصَٰرُ وَهُوَ
يُدۡرِكُ ٱلۡأَبۡصَٰرَۖ وَهُوَ ٱللَّطِيفُ ٱلۡخَبِيرُ ١٠٣ قَدۡ جَآءَكُم
بَصَآئِرُ مِن رَّبِّكُمۡۖ فَمَنۡ أَبۡصَرَ فَلِنَفۡسِهِۦۖ وَمَنۡ عَمِيَ فَعَلَيۡهَاۚ
وَمَآ أَنَا۠ عَلَيۡكُم بِحَفِيظٖ ١٠٤ وَكَذَٰلِكَ نُصَرِّفُ ٱلۡأٓيَٰتِ
وَلِيَقُولُواْ دَرَسۡتَ وَلِنُبَيِّنَهُۥ لِقَوۡمٖ يَعۡلَمُونَ ١٠٥ ٱتَّبِعۡ
مَآ أُوحِيَ إِلَيۡكَ مِن رَّبِّكَۖ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَۖ وَأَعۡرِضۡ عَنِ ٱلۡمُشۡرِكِينَ
١٠٦ وَلَوۡ شَآءَ ٱللَّهُ مَآ أَشۡرَكُواْۗ وَمَا جَعَلۡنَٰكَ عَلَيۡهِمۡ حَفِيظٗاۖ
وَمَآ أَنتَ عَلَيۡهِم بِوَكِيلٖ ١٠٧ وَلَا تَسُبُّواْ ٱلَّذِينَ يَدۡعُونَ
مِن دُونِ ٱللَّهِ فَيَسُبُّواْ ٱللَّهَ عَدۡوَۢا بِغَيۡرِ عِلۡمٖۗ كَذَٰلِكَ زَيَّنَّا لِكُلِّ أُمَّةٍ
عَمَلَهُمۡ ثُمَّ إِلَىٰ رَبِّهِم مَّرۡجِعُهُمۡ فَيُنَبِّئُهُم بِمَا كَانُواْ يَعۡمَلُونَ
١٠٨ وَأَقۡسَمُواْ بِٱللَّهِ جَهۡدَ أَيۡمَٰنِهِمۡ لَئِن جَآءَتۡهُمۡ ءَايَةٞ لَّيُؤۡمِنُنَّ
بِهَاۚ قُلۡ إِنَّمَا ٱلۡأٓيَٰتُ عِندَ ٱللَّهِۖ وَمَا يُشۡعِرُكُمۡ أَنَّهَآ إِذَا جَآءَتۡ
لَا يُؤۡمِنُونَ ١٠٩ وَنُقَلِّبُ أَفۡـِٔدَتَهُمۡ وَأَبۡصَٰرَهُمۡ كَمَا لَمۡ
يُؤۡمِنُواْ بِهِۦٓ أَوَّلَ مَرَّةٖ وَنَذَرُهُمۡ فِي طُغۡيَٰنِهِمۡ يَعۡمَهُونَ ١١٠



**(102) Ya ku mutane wannan mai waxancan siffofi shi ne Ubangijinku, baku da wani Ubangiji ba shi ba, babu abin bauta wa da gaskiya wanda ba shi ba, Shi ne mai samar da dukkan komai, ku bauta masa shi kaxai, Shi ne wanda ya cancanta da bauta, Kuma shi mai kiyaye dukkan komai ne. (103) Gannai ba sa iya kewaye shi. Allah tsarki ya tabbata a gare shi shi ne yake riskar gannai, ya kewaye da su. Kuma Shi ne mai tausasawa ga bayinsa nagartattu, kuma Masaninsu. (104) Yaku mutane hujjoji bayyanannu sun zo muku daga Ubangijinku, duk wanda ya hankalce su, ya sunkuya musu, amfanin haka gare shi zai koma, wanda ya makance daga gare su, bai hankalce su ba, bai sunkuya musu ba, to cutar a kansa zata qare. Ni ba mai kula da ku ba ne, mai qididdiga ayyukanku, kaxai ni Manzo ne daga Ubangijina, kuma Shi ne mai kula da ku. (105) Kamar yadda muka faxi dalilai da hujjoji kala-kala a kan ikon Allah, haka muke cancanza ayoyin alqawarin ni'ima da azaba da wa'azi kala-kala. Mushirikai za su ce,: "Wannan ba wahayi ba ne, kawai ka karanta shi ne daga ma'abota littafi da suke gabaninka", kuma don mu bayyana wa mutane gaskiya, da wannan cancanzawar waxannan ayoyi ga muminai daga al'ummar Annabi Muhammad (S.A.W), saboda su ne suke karvar gaskiya, kuma suke bin ta. (106) Ya kai wannan manzo ka bi abin da ake maka wahayi daga Ubangijinka na gaskiya, Allah (S.W.T) babu wani abin bauta, wanda ba shi ba. Kada ka shagalar da zuciyarka da kafirai da taurin kansu. Lamarinsu yana wurin Allah. (107) Da Allah ya ga damar kada wani ya yi shirka da ba wanda zai yi shirka. Ya kai wannan Manzo bamu sanya ka mai kula da qididdige ayyukansu ba, haka nan kai ba mai gadinsu ba ne, kaxai kai Manzo ne, babu abin da yake kanka sai isarwa. (108) Ya ku muminai kada ku zagi gumakan da mushirikai suke bauta wa tare da Allah, duk da cewa wadannan gumaka wulaqantattun abubuwa ne, waxanda suka cancanta a zage su, don kada mushirikai su zagi Allah da girman kai, da jahiltar abin da ya dace da Allah. Kamar yaddda muka qawatawa waxannan abin da suke kai na vata, haka muka qawatawa kowace al'umma ayyukanta, alheri ne ko sharri, suka yi abin da aka qawata musu, sannan ga Ubangijinsu za su koma ranar alqiyama, ya basu labarin abin da suke aikata wa a duniya, ya saka musu a kai. (109) Mushirikai suka yi rantsuwa da Allah, rantsuwa mai tsanani, wadda za su iya, suka ce,: "Tabbas in Muhammad ya zo da aya daga ayoyin da muka ba da shawara to zamu yi imani da su". Ka ce musu – Ya kai wannan Annabi -: "Ayoyi ba a wurina suke ba, ballantana in saukar da su, daga wurin Allah suke kaxai, yana saukar da su a lokacin da ya ga dama, kuma me ya sanar da ku – ya ku muminai – waxannan ayoyi idan sun zo a yadda suka ba da shawara ba za su yi imani ba?". Za su tsaya a kan girman kansu da jayayyarsu, saboda ba sa son shiriya. (110) Muna jujjuya zukatansu da ganinsu ta hanyar kange su tsakanin ayoyin da shiriya da gaskiya, kamar yadda muka kare tsakaninsu da imani da Alqur'ani a tun farkon lamari, saboda taurin kansu. Muna qyale su a cikin vatansu da borensu ga Ubangijinsu, suna ruxaxxu masu fagauniya.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - Tsarkake Allah daga zalunci da aqidar jabru take tabbatarwa. Ita ce cewa kafircin bayi da shirkarsu wani lamari ne da yake faruwa a bisa zavinsu. 2 - Ba wani Annabi daga cikin Annabawa da yake da iko ya zo da aya daga wajensa, ko lokacin da ya ga dama. Dukkan wannan lamari ne da yake wajen Allah Maxaukakin Sarki, shi kaxai yake da iko a kan haka, kuma shi ne mai hikimar da yake qaddara irin ayar da za ta zo da lokacin da za ta bayyana. 3 - Hana zagin allolin mushirikai, don gudun varna babba, ita ce qetare iyaka da zagin Allah, Ubangijin talikai. 4 - Allah yana iya kange bawa daga shiriya, ya kawar da ganinsa da zuciyarsa daga kan xa'a, don yi masa uquba a kan zaven kafirci da ya yi.**